Idan ba numfashi dayake ba sai kace gawa ce
Fashewa da kuka tayi
Daddyn baby ya riketa yace
Amma kin mini alkawarin bazaki yi kuka ba ko?
Girgiza kai tayi tace
Ji halin dayake ciki
Ajiyar zuciya mai martaba yayi yace
Yanzu wane hali yake ciki
Daddy hamma yace
Likitan yace
At any time zai iya farkawa
Shiru dakin yayi
Salim ne ya turo kofa ya shigo
Kallon daddy hamma yayi yace
Daddy likita nasan ganinka
Har ya mike sai kuma ya koma ya zauna ya kalli baffa yace
Kaje kai
Murmushi baffa yayi yace
Babu komai kaje kai
Tashi yayi ya tafi
Bayan ya dawo yace
Likitan yace
Akwai wani babban doctor da zai zo daga India ranar laraba zai duba shi amma suna sa ran ko zuwa anjima ya farfado
Shiru dai har zuwa yamma
Daddy ya kalli mamie yace
Tashi mu wuce kada dare yayi

Kallonshi mamie tayi tace
To
Haidar hade rai yayi
Murmushi daddy yayi yace
Dama bazance kazo muje ba ai ka wani hade rai
Sai da ya bawa kowa dariya
Washegari da safe da salim da haidar suka tafi sarina
Sun hado komai sannan suka taho da inna Mari da inna hadiza sai indo
Audu kuwa sai gobe idan baffa ya koma
Suna zuwa suka tarar da mai martaba sunzo domin gidan sarkin kano suka je da safe
Anan suka zauna har zuwa yamma babu wani labari
Washegari laraba suka likitan yazo
Bayan ya gama bincikensa yace
A gaskiya kwakwalwarsa lafiya lau take haka gangar jikinsa
Bashuda internal injuries haka ma external to mai yahanashi farkawa?
Mai martaba yace
Inajin zamu wuce dashi can adamawa  idan har abin. Yaci tura
Likitan yace
Eh to amma bazaku sami wani bayani sama da wannan ba
Girgiza kai kawai mai martaba yayi
Bayan bakon likitan ya tafi
Suka zauna sukayi shiru
Daddy hamma yace
Mai martaba kozan tafi dashi can India ko Allah zai sa adace
Girgiza kai mai martaba yayi yace
Kada ka damu za ayi masa na musulunci anan
Washegari daddy hamma da ammar suka koma India
https://www.facebook.com/groups/1569379426621615/
GOLDEN PEN WRITERS ASSOCIATION💫💫💫

❄We beare's of soo golden a pen,We writer's assiduously percieven No pain,so Magical Our creative golden pen,Be hold our worlds,A product of our pen savour Our worlds for it will  cause u no pain

📑farouk ko haidar📑

Written by deeja one love🖊️

Dedicated to madina m umar🌹

44-45

Mai martaba kuma sai washe gari,Da safe Abba da mama suka iso kowa yaga halin da ya ke ciki sai ya tausaya masa Humaira kuwa kullum batada aiki sai na kuka
Su salim kuwa saida daddy ya tsaya ya nuna musu bacin ranshi sosai sannan suka koma wajen service dinsu  Amma fa koda yaushe hankalinsu na kanshi  Kwananshi goma sha biyar daddy yace Akwai wani malami abokonshi a kaduna mai zai hana  a koma dashi can Haidar yaji dadin hakan sosai da sosai
Yau suka gama services dinsu kowa na murna amma su nasu da sauki
Salim kuwa a ranar suka tafi kaduna shida haidar
Akan nanda two weeks zasu dawo domin graduation.
Saukar hajiya salma daga flight ta Kira mai martaba aka tura mata dogarai da driver suka daukota
Fada ta fara wucewa tayi gaisuwa sannan ta shiga wajen fulani
Bayan sun gaisa fulani tace  Sai kukaji abu Mara dadi Hajiya salma ta marairaice fuska tace
Uhum wallahi abu babu dadin ji kwata kwata allah ya kyauta gaba
Fulani tace
Ameen dai
Haka ma data shiga wajen yafindo hari
Itama sai da tayi Mata jaje
Sannan ta karasa wajen uwar gijiyarta
Da murna ta karasa
Rungume juna sukayi cikin farin ciki
Bayan tayi wanka taci abinci ta kwanta barci sai bayan la'asar ta farka
Hajiya salma ta kalli yafindo karima tace
Wai mama ya akayi hakane?
Yafindo karima tayi dariyar mugunta tace
Zo ki Gani
Bedroom suka shiga
Wata karamar tukunyar kasa ta bude tasa hannu ta ciro wani abu kamar kwallo kuma transparent
Da mamaki hajiya salma tace
Wannan menene?
Yafindo karima tace
Wannan shine rayuwar farouk matukar tana cikin nan to bazai taba Tashi ba
Dariya hajiya salma tayi tace
Kai mama malam ne ya baki ko kuwa?
Yafindo karima tace
Wane malam wani na sake
Tafawa sukayi da hajiya salma tace
Kice mama wannan gama aikine
Yafindo karima tace
Kamar kinsani yar uwa amma fa da sharadi
Hajiya salma tace

Meye sharadin?
Yafindo karima tace
Zaki kai kanki wajensa ma'ana zaki bashi kanki(🙊)
Murmushi tayi tace
Babu matsala allah ya kaimu gobe
Ai ni indai bukata zata biya to ko meye zan aikata
Jira nake agama da wannan ma sai mu koma kan wancan idan yaso daga baya naji da ubansu shi fa atunanunshi son yaranshi nakeyi
Dariya suka Kara shekewa dashi  suka tafa kamar wasu kawaye(allah ka sa mufi karfin zuciyarmu ameen)
Washegari suka tafi wajen malam din
Babu laifi yanada tsafta watakila ko dan yana cikin garine oho
Yafindo karima a waje ta tsaya ita kuma ta shiga ciki
Wajen awa uku sannan ta fito a hargitse
Da mamaki yafindo karima ta kalleta
Cikin matukar galabaita tace
Mama muje gida kawai
Tun a hanya  tafara barci Dan haka suna komawa ta kwanta bata farka ba sai bayan magrib.
Tana cin abinci tace da yafindo karima
Gobe zan je Zaria daga nan zan shiga kano a matsayin zan duba wancan Dan iskan yaron.
Dariya yafindo karima tayi tace
Hmm aike kam naga kinfi tsanarshi ne da sauri tace eh mana.
Firarsu suka cigaba.
Washegari da wuri ta shirya ta tafi
Amra kuwa sai murna take yau mamanta zatazo
Yaya muhammad ya kalleta ya tabe baki  sai daf da isha tazo
Amra ta shirya komai sai murna take kamar me
Sun sha fira sosai sannan ya muhammad ya dauketa ya kaita wajen mama kasancewar basuda nisa da juna
Acan ta kwana
Washegari Abba yace dama suma sunaso su koma Dan haka su mama suma suka shirya
Suna isa kano asibitin murtala suka wuce Domin can akayi transfer dinshi
Gaskiya duk Wanda yaga halin dayake ciki sai ya tausaya mishi
Domin idan ka ganshi zakace barci yakeyi sai dai fa rama dayayi.
Cikin tausayawa mama tace
Allah ya yaye maka
Hajiya salma tace
Ameen.
Suna zaune su salim suka shigo
Da kallo mama ta bisu su kansu duka sun rame kadama salim yaji labari Dan shi dama bai iya sa abu araiba.
Gaishe dasu sukayi sannan mama ta Kara musu nasiha akan su Kara hakuri cuta ba mutuwa bace

Haidar yayi ajiyar zuciya yace
Nanda next week ma zamu wuce adamawa ai
Ok allah ya kaimu but dan allah Ku Kara hakuri kunji Allah zai bashi lafiya
Jinjina kai sukayi
Haidar ya kaisu sarina domin sure gaisa da sure baffa
Hajiya salma dai ruwa batasha agarin ba ta tattara ta tafi
Ita kuma mama sai da akayi magrib sannan suka tafi.
Haidar kuwa a sarina zai kwana tunda yanzu shifting sukeyi idan haidar ya kwana yau gobe salim jibi audu
Sai dai wajen juyashi da goge masa jiki shine sai  da safe idan wani yazo acikin su sai su hadu su biyu suyi.

Bayan sati daya mai martaba ya zo aka shirya aka maida su adamawa
Koda aka maidashi adamawa abubuwa sunyi sauki tunda yanzu sukan hadu suyi jinyarshi da yawa
Faisal kam tuni ya fara aiki amma su haidar mai martaba babu fadan da be musu ba amma sunce su bazasuyi aiki ba tareda farouk ba
Bayan an kwana biyu ya sake tarasu ya Nuna musu yanzu sun girma fa ya kamata susan da hakan
Duk yadda ya bullo musu abu ya gagara karshe harya fusata yace
Kamar baku yarda da kaddara ba yanzu kuma idan mutuwa yayi fa ?
Kuka salim ya fara mishi yana fadin bazai mutu ba
Haidar kam tabe fuska yayi
Ganin abin Nasu da gaske sukeyi yasa ya tattara ya zuba musu idanu
Sun je aiken da mai martaba yayi musu sun dawo
Haidar ya ajiye maganin akan bedside table ya shiga wanka
Salim kuma ya kwanta
Kamar a mafarki yaga idanun farouk na neman budewa
Cikin farinciki  ya fara kwalawa haidar Kira
Ba shiri haidar ya daura towel ya fito.
📑farouk ko haidar📑

https://www.facebook.com/groups/156937
*📑FAROUK KO  HAIDAR* 📑

*~GOLDEN PEN WRITERS ASSOCIATON~💫💫💫*

https://www.facebook.com/groups/1569379426621615/

*~❄we beare's of soon golden we writer's assiduously percieven No pain so magical Our creative golden pen Be hold our worlds A production of our pen savour Out worlds for it cause u np pain~*

written🖊️ By Deeja One Love

Written by deeja one love🖊️

Dedicated to madina m umar🌹

46-47
A hankali ya bude idanunshi
Maidawa yayi ya lumshe idanun domin haske yayi mishi yawa
Da sauri salim ya tafi sanar da su mai martaba.
Cikin farin ciki suka taho
Kowa so yake yayi mishi magana amma abu ya gagara domin koya bude baki da nufin yin magana sai abu ya gagara
Hamdala mai martaba yayi yace
Da alamu sauki ya fara samuwa
Kan lokaci kankani har labari ya bazu a family haidar ya bude idanu.
Kowa murna yakeyi domin sauki ya fara zuwa
Momma kuwa tanaji har hawayen farin ciki sai da tayi
Daddyn baby ya na ta tsokanarta
Murmushi tayi tace
Ni dai idan allah ya kaimu gobe zamuje ko?
Kallonta yayi yace
Da wannan cikin naki zakije a'a gaskiya sai kin haihu
Shiru tayi bata kuma cewa komai ba
Daddare tana zaune Tana tsefewa baby kai.
Mararta taji ta murda Mata cikin dabara ta zame kan baby ta mike
A bedroom ta sami daddy yana aiki da laptop
Kallonta yayi Cikin kulawa yace
Ya dai ko da matsala ne?
Girgiza kai tayi
Kan ta yunkura juwa ta kwasheta
Da sauri daddy ya tarota
Daukarta yayi cak ya nufi parking lot da ita.
Koda suka isa hospital da sauri aka amsheta
50mins ta haifo yaranta guda biyu duka Mata
Bakin daddyn baby ya kasa rufuwa
Sai buga waya yakeyi

Salim na zaune yana Danna waya kiran daddyn baby ya shigo
Kallon haidar yayi dayaketa shakar barcinshi
Daga wayar yayi
Cikin farin ciki yace
Mamanku ta haihu
Ihun murna salim yayi.
Cikin sauri salim ya bude ido yana mazurai
Kallon salim yayi ya dalla mishi harara
Yace
Kai dai wallahi akwai banza Muna barci kawani tasheni
Kafin salim yace wani abu an bude kofar an shigo
Yafindo hari
Cikin sauri salim ya rungumeta
Da haidar da farouk zuba musu idanu
Da mamaki salim yace
Wai mai ya faru ne?
Salim ya washe baki yace
Momma ta haihu
Da gudu haidar yazo ya rungume salim
Murna kam ba'a magana
Farouk kuwa da idanu yake binsu.
Ga abin murna amma babu dama
Murmushi yayi
Haidar yace
Lah! Ji nawan yana murmushi
Ranar dai Kwanan farin ciki familyn sukayi
Washe gari da wuri yafindo karima da yafindo hari suka tafi taraba
Ana sallamota daga hospital suka wuce da ita adamawa.
Suna isowa suka sami gida ya cika da yan uwa
Kowa na kokarin daukar yaran
Hannun haidar ta rike tace
Ina dan uwanka
Murmushi daddyn baby yayi yace
Muje ki huta sai kije anjima mana
Daga kai tayi badan ranta yaso ba
Bangaren fulani ya kaita
Ruwa mai sadi tayi wanka dashi
Kafin ta fito an ajiye mata tuwon dawa da miyar kubewa yaji man shanu
Sai da taci ta koshi sannan ta kwanta
Daddyn baby da yafindo hari suka shigo da babies a hannunsu
Ajiyesu sukayi
Yafindo hari ta juya ta fita
Kallon daddyn tace

In taso muje ka kaini wajen farouk din?
Murmushi yayi yace
Ina zuwa
Bai dade ba suka dawo tareda fulani
Yace
Fulani ga yaran nan zamuje ta dubo farouk
Fulani tace
Kekam ki bari ki huta mana
Daddyn baby yace
Fulani Barta muje kawai idan ba haka ba yau bazata barni na huta ba
Murmushi fulani tayi tace
Adawo lafiya
Har bangaren mazan ya kaita
Salim yana kwance yana barci
Haidar kuma yana wanka
Da idanu ta bishi yayi haske sai dai ya rame
Murmushi yayi Mata
Hannunshi ta rike tace
Ya jikin
Lumshe idanu yayi ya bude
Haidar daya fito daga bayi yace
Momma har kinzo ganin jikinshi
Daga kai tayi alamar eh
Ya Dora da cewa
Ai ma ya sami sauki
Kallon salim yayi ya daka.mishi duka yace
Tashi kallallaba
Harararshi farouk yayi ya kauda kai
Momma tayi dariya tace
Ah lallai jiki da sauki tunda an iya harara
Duka sukayi Dariya
Yafindo karima ta kira hajiya salma tace
Kinji rumaisa ta haihu
Hmm naji mana jiya.mijinta ya kira hamma ya gaya mishi.
Ta gaya cikin takaici
Yafindo karima tace
To yaushe zakuzo
Nisawa tayi tace
Sai ranar laraba
Allah ya kaimu dole idan kinzo mu koma wajen malam din nan
Ana Jibi suna su ammar da mutanen kano sukazo
Yan zaria da yan kaduna suma sunzo
Gida ya cika masha Allah

Ammar ya kalli amra yace
Ki bari anjima idan aka tafi sallar magrib sai mu duba
Jinjina kai tayi alamar to
Da yamma yafindo karima tace
Bari zuwa anjima mu karasa shi
Su kuma yaran gobe idan an gama taron suna
Murmushi hajiya salma tayi tace
Ai gwara ayi ta ta Kare kawai
Ana kiran sallah kowa yana haramar shiga masallaci
Amra ta Kira ammar tace
Bro yafindo karima ta shiga toilet kayi sauri
Yana ajiye wayar cikin sauri ya kalli faisal yace
Ka tanaji ashana kazo wajen garden
Da sauri yace
To
A bakin kofar ya tarar da amra
Kallonta yayi yace
Muje
Suna shiga suka fara bincike bincike
Kaf duk Indiana suke tunanin gani sun duba amma basu ganshi ba
Amra ta tsugunna kasan gado ta janyo wani akwati
Cikin sauri ta bude ta ciro kayan ciki
Da sauri suka fice
A garden suka Tarar da faisal zube kayan sukayi
Wannan karamar randar
Ammar ya daga
Yafindo karima ta fito daga bayi
Kallon gadon tayi
Zaro idanu tayi ta dafe kirji
Da sauri ta leka window
Ganin aika aikan da su ammar suke shirin yi yasa ta kwallara kara
Dai dai lokacin dasu mai Martaba suka dawo masallaci
Jin Kara yasa suka nufi garden
Suma dake cikin fada suka fito da gudu
A rikice yafindo karima ta zubo da gudu tana fadin kada ka fasa
Zaro idanu hajiya salma tayi itama tace
Ammar kada ka aikata
Su mai martaba kallonsu kawai sukeyi domin basu fahimci me ake nufi ba
Ammar ya kalli faisal yace
Action
Murmushi yayi ya banka musu wuta
Ammar ya bugata da kasa ta tarwatseee

*📑FAROUK KO  HAIDAR* 📑

*~GOLDEN PEN WRITERS ASSOCIATON~💫💫💫*

https://www.facebook.com/groups/1569379426621615/

*~❄we beare's of soon golden we writer's assiduously percieven No pain so magical Our creative golden pen Be hold our worlds A production of our pen savour Out worlds for it cause u np pain~*

written🖊 By Deeja One Love

Bashier sufyein ina gaisuwa sosai duk da kwana biyu naji shiru Allah ya kara hazaka yasa kafi haka
Ameen
48-49
Gidan gaba daya yayi baki wani bakin hayaki ya fara fita daga cikin fasashshiyar tukunyar
Ihu yafindo karima  tayi lokaci guda fuskarta ta koma baka.
Farouk kuwa ji yayi kamar an kwanceshi daga daurin da aka masa
Cikin sauri ya mike ya fito
Ganin harabar gidan babu kowa yasa shi nufar garden
Yana isa wajen yafindo karima tayi ihu ta shaki wuyan hajiya salma tana fadin
Sun lalata mana komai kinga abinda yaranki sukayi mana
Mun shiga uku zamu mutu
Na gaya miki zamu mutu.
Hajiya salma kuwa idanu yayi jajir domin ba karamar shaka tayi Mata ba
Cikin sauri su hajiya zainab suka kwaceta
Ihu ta kumayi ta fara fuzge fuzge
Duk wani kulle kulle da sukeyi sai da ta fada tanayi tana soshe soshe
'Ya'yanta kuwa kuka suka farayi
Mai martaba ya bawa doagarai umarnin da su kamata su kaita cikin turu.
Mai martaba ya dubi mutanen wajen yace
Kowa ya shigo ciki
Bayan kowa ya zauna daddyn yola yace
Salma munaso muji meke faruwa? ko kuma nace mai ya faru?
Kuka ta fashe dashi tace
Dan Allah Ku yafe mini wallahi nayi nadama
Daddyn yola ya daka Mata tsawa yace
Tambayarki fa akayi mai ya faru?
Hawaye ta share tace
A lokacin da mahaifinmu ya rasu muka dawo nan gidan tun lokacin nakeson hamma

Sai dai hankalinshi kwata kwata baya kaina yana kan yar uwata
Ganin hakan yasa na fara kishi da ita
Nayi bakin ciki lokacin da akayi bikina da abbansu ammar
Amma duk da haka ban saduda ba kuma ban Dena son hamma ba
Lokacin da akayi auren rumaisa da hamma naji bakin ciki sosai sai dai babu yadda zanyi
Ana haka watarana mama ta kirani a waya kan ta sami wani malami da zai mini aiki mun dade muna ja in ja da ita kafin na amince
Farkon aikin daya fara mana shine kashe abbansu ammar
Domin babu yadda za'ayi na auri hamma ba tare da aurena ya mutu ba
Bayan malamin ya tura aljani ya kasheshi sai mukaji labarin rumaisa nada ciki ansha tura Mata aljani ya sace cikin amma abu ya garara saboda yawan addu'arta
Da hakan bai samu ba sai muka sa aka kwance tayar motarta duk da haka muka bita abaya nida mama har sai da muka ga konewar motar sannan muka juya muka koma wajen malamin
Aranar ya bani maganin da nasawa hamma har ya fara sona
Abin ya bamu mamaki da mukaji bata mutu ba
Alokacin mama tace mu koma a kasheta sai dai na nuna a'a
Hakadai har tayi convincing dina akan cewa idan fa ban kasheta ba to lallai har yanzu sunada abinda ya hadasu wato 'ya'ya
Wannan yasa na yarda domin banason abinda zai hada hamma da rumaisa
Wannan yasa muka koma ya bamu magani akan mu sa Mata a abinci hakan zai Kara Mata kiyayyar hamma kuma zai sa tayi duk abinda muka sata
Sai layar da muka binne Wanda hakan shine zai sa bazata taba cewa mu muka sata ta yar da yaran nata ba
Haka kuwa akayi muka bawa zainab ta sa Mata a abinci ta kuma ci
Ni na Kira ta a waya tace da ita akan ta cewa halima zata taho
Babu musu tace to
A hanya mama ta tareta suka je kaduna suka fara bayarda haidar sannan suka wuce kano suka bayar da farouk kuma mu muka tsara abin ya zama kamar hatsari ne.
Duk da haka bamu kyalesu ba mama ta kuma cewa mu koma wajen bokan a samusu ciwon da zai dinga wahalar dasu
Haka muka koma wajenshi ya bamu amma da sharadin cewa duk ranar da asirin mu ya tonu to daya daga cikin mu zai haukace
Haka muka yarda dan a tunanin mu asirinmu bazai taba tonuwa ba
Mun so a tura musu aljanune sai dai inda suke akwai kariya sosai wannan yasa hakan bai yiwu ba
Duk da haka sai akayi amfani da yawan zuciyar farouk aljanun suke shafarshi shi kuma haidar sai akayi amfani da yawan  kallace kallacenshi aka turo wanda suke taba idanunshi
Ta kwashe sauran abinda ya faru ta gaya musu
Tsit wajen yayi
Sunkuyad da kai tayi tace
Dan Allah ina neman yafiyarku Ku yafe mini
Amra ta mike tace
Wallahi bazai taba yiwuwa ba kullum kina yaudarar mu akan mahaifinmu rasuwa yayi

Ashe kasheshi kikayi ashe ba sonmu kike ba
Daddyn yola yace
Ya isa haka amra koma ki zauna
Komawa tayi ta zauna tana Kuka
Kowa shiru yayi yana jiran hukuncin da mai martaba zai yanke
Gyaran murya yayi yace
Alhamdulillahi abubuwa sun faru da yawa a wannan familyn to mu godewa allah da hakan ya faru domin idan har yana sonka ne sai ya jarabceka
Dan haka komai ya faru zamu dauka a matsayin jarabawa
Ni yanzu bazan yanke muku hukuncin komai ba sai dai zan barku da Allah shi yasan mai. Yafi dacewa daku
Sannan magana ta karshe shine nidai allah ya gani koda Dan uwana ya mutu ya barku nayi dai dai iya yanda zanyi Ku sami kyakkyawar tarbiya Allah kuma yana sheda
Don haka tunda hakan ya faru zaki koma bayan gida da zama sannan ki nemi yafiyar wa'inda Kika yiwa laifi idan sun yafe miki shikenan
Ran da kika kashe shi kuma keda mahaliccinki.
Yana gama fadan hakan ya mike yayi cikin gida
Tashi tayi tana kuka ta dubi daddy hamma da rumaisa tace
Dan Allah Ku yafe mini
Ajiyar zuciya daddy hamma yayi yace
Allah ya yafe mana gaba daya
Ita ma momma abinda ta fada kenan
Su haidar da farouk ta duba tace
Nasan na cutar daku sosai na raba mahaifiyarku da mahaifinku na rabaku da juna na raba Ku da lafiya amma duk da haka ina neman yafiyarku
Haidar yayi murmushi yace
Komai ya wuce mummy Allah ya yafe mana
Farouk yayi ajiyar zuciya yace..............
*📑FAROUK KO  HAIDAR* 📑

*~GOLDEN PEN WRITERS ASSOCIATON~💫💫💫*

https://www.facebook.com/groups/1569379426621615/

*~❄we beare's of soon golden we writer's assiduously percieven No pain so magical Our creative golden pen Be hold our worlds A production of our pen savour Out worlds for it cause u np pain~*

Written🖊️by deeja one love

Dedicated to madina m umar🌹
50-51

A sanyaye farouk yace
"Allah ya yafe mana gaba daya",kowa yaji dadin abinda ya fada.

Sai da aka kai ruwa rana sannan amra da ammar suka yafewa mahaifiyarsu.

Sai da suka koma bangarensu sannan salim yace
"Ashe farouk ya farfado".

Dariya haidar yayi yace
"Baka ganshi ba sai yanzu",Murmushi kawai yayi yace
"Kyaleshi haidar neman magana ne kawai kalar nashi".

Matsowa salim yayi yace
"Wai ya akayi ka Tashi ne?,Shiru farouk yayi.

A ranar cikin farin ciki suka kwana,sai dai da safe aka wayi gari da yafindo karima ta mutu,
Mutuwar da ta sa jikin mutane da yawa yayi sanyi.

Bayan anyi suna hassanar aka sa mata sunan inna Mari wato mariya suna ce Mata islam,hussaina ita kuma taci sunan mamie wato khadeeja suna ce Mata iman.

Suna yayi yadda ake so sai dai muce Allah ya raya Islam da iman.

Bayan kwana biyu da suna kowa ya fara shirin tafiya ,
Haidar da salim sun tafi kasuwa domin siyayya,farouk kuma yana kwance.

Momma tayi sallama ta shigo kallonshi tayi tace
"Mai yasa bazaku zauna anan ba?

"Saboda can yafi dadin zama"
Ya bata amsa atakaice.

Shiru tayi na Dan lokaci kan tace
"Saboda me kace haka?".

"Saboda can babu hayaniya da yawa "
Ya Kara bata amsa .

Riko hannushi tayi tace

"To farouk mu tafi taraba tare mana"

Murmushi yayi yace
"Momma duk yadda zamuyi bazai yiwu ba saboda su baffa da daddy gani zasuyi kamar ke muke so mu dawo wajenki;
Jinjina kai tayi alamar ta gamsu
Farouk ya Dora da cewa
"Kidai bari kawai mu dinga kawo miki ziyara amma bazai yiwu ace Dan mun hadu da iyayenmu ba muce zamu juya musu baya".

Numfasawa tayi tace
You have a point.

Fira suka cigaba da yi har su haidar suka dawo ,
Nan suka dinga shirmensu ,
Farouk dai murmushi kawai yakeyi
Momma ta girgiza kai tace
"Ku wallahi bakwa girma har yanzu kuna abu kamar kananan yara"
Ta mike ta fita.

Washe gari da wuri suka dauki hanya,sai da suka ajiye su farouk a kano sannan suka wuce,ana zuwa Zaria su salim suma suka wuce gida.

Bayan wata biyu daddy hamma ya fara Gina musu tafatsetsen hospital a cikin garin yola, daddyn yola yaso ya sama musu aiki amma sukace su basa son na gwamnati abarsu da private din da daddy ke gina musu.

Yanzu indo anzama yan Mata ta Kara wayewa sosai, Dan lokaci zuwa lokaci takanje Zaria ko kaduna har taraba ma wajen momma,
Su Islam kuwa watansu uku amma sunyi Wayo sosai da sosai.

Shekara mai zuwa indo zata zana waec da neco hakan yasa farouk ya dage da koya Mata abubuwan da bata Sani ba.

Farouk ya gama shirin shi na zuwa Zaria
Indo ta shigo dakin daga bakin kofa ta tsaya.
Hade rai tayi kallonta kawai yakeyi yana murmushi.

Hawaye ya gangaro daga idanunta still kallonta kawai yakeyi,ganin yaki cewa komai yasa ta fara bubbuga kafa a kasa
Kusa da ita ya matso yace
"Humaira tsaya kiji".

Girgiza kai tayi ta turo baki gaba tace
"Nidai kawai yaya farouk kaje dani"

Ajiyar zuciya yayi yace
"To jeki shirya kayanki".

Tsallen murna tayi da sauri ta juya ta tafi,girgiza kai yayi yace
"Humaira rigima ".

Cikin lokaci kankani ta gama shirinta cikin tsokana yace
"Wai ni na rasa mai kike zuwa yi Zaria kodai kinyi saurayi acan ne?,
Rufe fuskarta tayi tana dariya.

Sai karfe biyu suka shiga zaria a gidan hajiya zainab suka fara yada zango,
Cikin murna faisal yace
"Ah lallai wannan Karon anyi abin kai "
Murmushi kawai farouk yayi .

Sai da suka ci abinci suka huta,sannan faisal ya kwashesu a mota suka tafi gidansu salim,
a bakin get ya ajiye su sannan ya wuce wajen aiki.

Suna shiga ya samu husna da yusra suna ta dambe akan hijab,
Sun cika gidan da hayaniya,
Yanayin sallama kowacce ta natsu.

Yace
"Ina mama?
Da sauri sukace
"Ta tafi kasuwa amma bazata dade ba zata dawo",

"Ina salim"
Ya Kara tambayarsu,
"Yana bangarensu"

Be ce komai ba ya mike ya tafi har ya wuce ya dawo yace
"Ku cigaba da damun mutane tunda Ku bakusan me yake muku ciwo ba"
Sunkuyad da kai sukayi
"Oya bani hijab din"
Da sauri yusra ta mika mishi,
Amsa yayi kawai ya wuce.

Yana tafiya husna ta bata rai tace
"Wannan fa yazo kenan wallahi"
Humaira tayi dariya tace
"Ko na kirashi ne?
Cikeda kuluwa yusra ta harareta tace
"Kirashin mana",
Cikin tsokana humaira ta fara kwala mishi Kira,
Husna ta dau filo ta bita dashi humaira ta haye sama tana dariya.

Farouk kuwa yana zuwa ya sami salim sai sharar barci yakeyi ,
Ajiye jakarshi yayi ya shiga bathroom yayi wanka ,
Sai da ya gama shiryawa sannan ya tasheshi.

Da mamaki salim yace

"Yaushe kazo?
Harararshi farouk yayi yace
"Taya zaka San nazo kato da kai kazo ka kwanta kana shakar barci".

Dariya salim yayi yace
"Wallahi nagaji ne "
Farouk yace
"Wai ka gaji to me kayi daka gaji?
Salim yace
"Kai dai bazaka gane bane kawai"

Girgiza kai farouk yayi yace
"Shiyasa ai kaji dadi da har yanzu ba'a fara aiki ba ko",
Dariya salim yayi kawai.

Da yamma mama ta dawo ta tarar dasu farouk
Da farin ciki tace
"Maraba da mutanen kano, ai dama tunda naji gidan shiru babu hayaniyar wa'inann marasa jin nasan kazo"'
Murmushi kawai yayi.

Bayan sun gaisa ne tace
"Zakuje amsa kiran mai martaba ne?,daga kai kawai yayi.

Washe gari da wuri suka wuce kaduna,sun tarar da haidar yana hospital din su daddy.

Salim yayi dariya yace
"Kaga namiji jarumi",harara haidar ya galla mishi yace" kafa fita idona kallaba kawai",farouk ya harari haidar ya kauda kai.

Indo kuwa sai murna take domin kuwa tareda su husna suka taho,tunda tazo ko farouk ma bata nema ba,shima kuma haka be nemeta ba.

Da safe yaya adnan ya kwashe su sukaje gidan amare,bayan sun fito ne suka wuce companyn motoci kowa ya zabi wadda yake so,da farouk da salim kala daya suka dauka baka range rover sai haidar daya dauki camry new model 2008 ash in colour(ruwan toka).

Cikin farin ciki suka dawo gida,kowa ya tayasu murna,yaya adnan kuwa yasha godiya,murmushi kawai yayi yace"komai nayi muku ban fadi ba kannena".

Daddy yana dawowa suka bashi labari shima ya tayasu murna sosai.

Washe gari suka wuce adamawa kowa da motarshi,farouk ya dauki indo,salim kuma surayya da husna,haidar kuma sumayya da yusra.

Sun iso ana kiran sallar magrib wai a hakan ma sunyi sauri sosai(kun San dai yadda mutum yake idan aka bashi sabon abu especially abinda ya shafi ride😁).

Masallaci suka fara wucewa sai da sukayi sallah sannan suka shiga gidan,shidai farouk bangarensu ya wuce,da haidar da salim kuma bangaren fulani suka wuce.

Sai da yayi wanka sannan yaje ya samesu,shirmen da suka saba shi suke tayi dai,fulani nayi musu dariya.

Tsaki farouk yaja yace"wallahi kudai baku girma ,anan suka ci abinci sannan suka wuce bangarensu,wajen wankan ma sai da suka Kara raba hali sanana sukayi.

Ana idar da isha suka biya suka gaida sarki,cikin farin ciki ya tare su har yana Jan su da wasa.

Washe gari da safe bayan sun karya,wani dogare yazo ya tsuguna yace"ranku ya dade mai martaba na nemanku a falonshi"
Salim ya amsa da "kace muna zuwa"

Dogari yace"yace Ku taho da kannenku"
Salim ya kuma bashi amsa da to.

Sai da suka biya bangaren Mata na gidan suka dauki su sumayya sannan suka wuce,a zaune suka sameshi bangarenshi na dama fulani bangaren hagu kuma yafindo hari,sai faisal da ammar akasa,suma kasan suka nemi waje suka zauna.

Mai martaba yayi gyaran murya yace
Alhamdulillahi abinda yasa na kiraku shine kunsan dai cewa yanzu kune akan layi.

Haidar ya dago yace "layin me?,mai martaba yace"aure,dariya abin ya basu.

Da mamaki mai martaba yace"meye na dariya?ya isa haka kai ammar ga yar uwarka nan yusra,farouk ga humaira nan,haidar ga surayya nan,faisal ga husna nan,salim kaida sumayya.
*📑FAROUK KO  HAIDAR* 📑

*~GOLDEN PEN WRITERS ASSOCIATON~💫💫💫*

https://www.facebook.com/groups/1569379426621615/

*~❄we beare's of soon golden we writer's assiduously percieven No pain so magical Our

creative golden pen Be hold our worlds A production of our pen savour Out worlds for it cause u np pain~*

written🖊️ By Deeja One Love

Bashier matafiya uku munji shiru fa ya kamata a duba mu. 🙏🏻

52-53

Shiru sukayi domin basuda ta cewa,mai martaba yace"bakuce komai ba".

A sanyaye ammar"mun gode Allah ya saka da alkhairi.

Haidar zai yi magana faisal ya take masa kafa,dagowa yayi ya kalleshi shi kuma ya galla masa harara.

Murmushi mai martaba yayi yace"masha Allah naji dadi Allah ya muku albarka,da sauri suka Amsa da ameen.

Suna fita haidar yace"gaskiya banji dadi ba a rasa wacce za'a bani sai wacce muke sa'a,salim dariya ya dinga yi,cikin jin haushi ya bishi da gudu,ganin ya taho shima yasa gudu.

Faisal yace"ai wallahi za'ayi kallon shirme,shidai farouk bece komai ba.

Mai martaba kuwa daddyn yola ya Kira yace ya kira members na family nanda three weeks bikin su farouk,duk wanda aka Kira sai yayi murna idan yaji cewa tare da bikin bude asibitin za ayi.

Sai da suka Kara kwana sannan suka tafi taraba,kowa zolayarsu yake akan angwaye,duk da babu mai wata matsalar da azahirance sai haidar wanda a fili yake nuna bayaso,shi kuwa farouk nauyi abin yake mishi.

Momma cikin farin ciki ta amshesu,sai zolayarsu take,haidar ya tabe fuska yace"momma pls ki dena".

Salim yayi dariya yace "bakasan me ba wai salim da mata!,haidar yace"za'a ga shiririta",hararar haidar farouk yayi,yana dagowa suka hada ido da momma kauda kai yayi yana murmushi.

Da dare momma tayi sallama ta shigo,farouk ke duba takardu,,salim da haidar duka sunyi barci.

Murmushi farouk yayi yace"barka da dare momma",hannunshi ta rike tace "sannu da aiki",shiru sukayi na wani lokaci.

A hankali momma ta murza hannunshi tace"hadin yayi maka?,saukar da idanunshi kasa yayi yace"wanne fa?"

Murmushi tayi tace"Wanda mai martaba yayi"kallonta yayi yace"idan beyi ba za'a canza ne?daga kai tayi tace"idan har bakaso sai a canza",murmushi kawai yayi yace"momma kina nuna bambanci,"
Katseshi tayi tace"kamar yadda kake nunawa ko?,

Hannunta ya rike yace"ba haka bane haidar Dan uwanane awajen haihuwa tare aka haifemu haka zaman da mukayi a mahaifarki don haka duk wanda zanso a bayanshi yake.

Jinjina kai tayi tace"hakane na yarda da abinda ka gaya"tambayarta yayi yace"to ke me yasa kike nuna bambanci?,kanshi ta kwantar a jikinta tana sa hannu a cikin sumarshi.

Ahankali take shafa kanshi har barci ya daukeshi,murmushi tayi sannan ta gyara mishi kwanciya tayi addu'a ta shafa mishi,wajen haidar ta matsa shima addu'ar tayi ta shafa mishi,hakama salim,sannan ta kashe light ta fita.

Sai da akayi kiran sallar asuba sannan suka farka,koda suka idar da sallar suna dawowa barci suka koma.

Sai goma sannan suka tashi,wanka sukayi sannan suka fito domin karyawa,a dinning area suka samesu duka domin yau weekend ne.

Murmushi momma tayi tace"sai yanzu?
Dariya salim yayi yace"Allah momma kinsan nan yafi adamawa dadin zama,dariya sukayi gaba daya,farouk kuwa murmushi kawai yayi.

Daddyn baby yace"kaima zama da farouk ya sa kana neman kaki dangi ko?",haidar ya cuno baki yace"Damuwace kawai tayi yawa acan.

Da mamaki momma tace"adamawar?",daga kai haidar yayi yace"kullum busa ke tada mutum a barci kamar ana farauta,salim ya kara da cewa"ga kuyangu da bayi duk inda kayi ana damunka.

Daddyn baby yace"da har zan bawa mai martaba shawara akan cewa idan ya tashi murabus ya

dora ka,da sauri haidar yace"wa kenan?"gimtse dariyarshi daddyn baby yayi yace"kai mana,haidar da salim suka kalli Juna suka fashe da dariya.

Salim yace"da kuwa anga shiririta"hararashi haidar yayi yace"wallahi ka fita idona nine mashiriricin?"salim yayi dariya yace"eh mana ai hakanne"haidar ya daure.

Momma ta mikawa farouk tea tace"nidai Ku bar maganar haka shima tsokanarka yakeyi,haidar ya cuno baki yace"momma ai wallahi banason wannan tsokanar",salim ya kwashe da dariya.

Haka suka cigaba da shirmensu har aka gama breakfast din,baby da momma suka kwashe kayan.

Su farouk kuwa palour suka koma shidai farouk channel ya kamo na news,salim da haidar kuma suka cigaba da shirmensu.

Da yamma suka shirya suka fita,a wani mall suka fara tsayawa sukayi siyayya ,shidai farouk yana makale da humaira duk inda tayi yana binta,salim yace"mutumina kaga abinda Dan uwa yakeyi kuwa?"haidar yace"to sai me shi zai jawa kanshi raini",salim yace"to nima na tafi,

Haidar ganin kowa ya tafi nashi wajen yasa shi matsawa kusada surayya,harara ta aika mishi shima hararata yayi ya kauda kai,jin shirun yayi yawa yasa surayya ta nufi mota,ganin ta tafi yasa shima binta,a motar suka zauna har su farouk suka gama siyayyar suka taho.

Kowa motarshi ya shiga sannan suka dauki hanya wani garden suka tsaya,haidar ya hade rai yace
Meye haka kuma,hannu ya fito dashi ta glass ya musu nuni da lafiya?,salim ya nuna mishi Alama da su shiga.

Tsaki yayi sannan ya fito,itama surayya ta biyo bayanshi, kowanne wajen zama ya nema.

Farouk ya kalli indo yace"me za'a kawo miki?",sai da tayi fari tace"coke ma ya isa,kasa cewa komai yayi shikuwa waiter tafiya yayi domin kawo mata.

Farouk yace"waya koya miki?",tace"me kenan?
Dan juyar da kai yayi yana murmushi shidai yasan baya kin humaira haka baya jin xai iya zama da ita amatsayin matarshi.

Haidar ya dago ya kalli mutanen wajen yayi tsaki ya cigaba da danna phone dinshi,surayya itama tayi tsaki ta dauko wayarta ta danna ,kiran yusra tayi suka fara fira(kasancewar su kowacce mai martaba yace Wanda zai aureta shi zai kaita hakan yasa yusra take adamawa wajen ammar sai gobe zai kaita Zaria daga nan ya wuce India ita kuma husna yau suka tafi abuja da faisal sai gobe suma zasu wuce Zaria), haidar dai kallonta kawai yakeyi"wai wannan ita zai aure she is too pride😏!

Ganin bazasu tafi da wuri  bane yasa shi mikewa,a Mota ya tsaya jiran surayya,ita kuma ganin be ce Mata ta taso ba yasa tayi zamanta,ganin taki tahowa yasa yaja motar da sauri ya bar wajen.

Dariya salim yayi yace"Dan rainin Wayo",sumayya tace"meya faru wallahi no nasan za'ayi show mai dadin kallo a gidansu.

Farouk ya dubi ya salim da hannu ya nuna mishi alamun lafiya,salim ya daga kafada alamar be sani ba.

Farouk ya dubi humaira yace
"Zo muje kinga haidar has gone ya kamata mu wuce muma,murmushi tayi sannan ta mike.

Ganin duk sun mike yasa surayya itama mikewa,motar farouk ta shiga.

Koda suka je gida motarshi bata nan,da mamaki farouk yace"ina to yaje?"surayya ta tabe baki.

Koda suka shiga azaune suka tarar da momma,kunyace kuma ta kamasu,humaira dai bayan farouk ta boye,ita kuma sumayya tayi sama da gudu.

Momma tayi dariya tace"yaran zamani wato kun gama soyayyarku yanzu kuma zaku zo kuce kuna jin kunyata.

Shi kanshi farouk din kamar kasa ta bude ya shige haka yake ji,shafa fuskarshi yayi sannan yace"barka da yamma.

Amsawa tayi cikin farin ciki domin tasan sunyi na'am da zabin mai martaba kenan
*📑FAROUK KO  HAIDAR* 📑

*~GOLDEN PEN WRITERS ASSOCIATON~💫💫💫*

https://www.facebook.com/groups/1569379426621615/

*~❄we beare's of soon golden we writer's assiduously percieven No pain so magical Our creative golden pen Be hold our worlds A production of our pen savour Out worlds for it cause u np pain~*

written🖊️ By Deeja One Love

54-55

Momma tace"ina haidar ne?"farouk yayi saurin cewa ya biya ta wajen wani abokinshi ne.

Haidar kuwa sai dare sannan ya dawo,a tunaninshi duk sunyi barci Dan haka wanka kawai yayi ya kwanta.

Yana kwanciya farouk yace"da gaske baka sonta?,girgiza kai yayi yace"a'a kawai her pride extend the limit."

Dariya abin ya bawa farouk,murmushi yayi yace"Allah ya kyauta"ameen,haidar ya amsa.

Bayan sunyi break fast da safe momma tace"kuzo muje  wani waje"cikin farin ciki suka Tashi.

Unguwar dake gaba dasu kadan sukayi horn a dai dai wani gida,plat mai kyau,sai santi sukeyi dan dai-dai ne.

Haidar yace"momma nan ina ne?"hannun farouk ta rike tayi murmushi tace"gidan dana siyawa baffa ne inaso su dawo nan,farouk besan lokacin da murmushi ya subuce masa ba.

Sun zagaya gidan yayi kyau sosai kuma sunyi murna,salim yace"su humaira za'a shigo birni.

Murmushi kawai farouk yayi,haidar ya hade rai yace"momma kina ganin nawan ko bambanci yake nunawa.

Farouk ya kalleshi yace"me kuma nayi?",haidar ya harareshi yace "da nine na fadi abinda salim ya gaya da yanzu ka harareni,amma da yake Dan gwal ne murmushi kawai kayi.

Dariya salim yayi yace"jealousy",sumayya tace"Allah ko ni haka nake gani wallahi yaya haidar kada ka yarda,harararta salim yayi yace"waya saka baking",haidar yace"gulma fa"tsaki surayya tayi tace"Allah ya Kara"

Kafarta haidar ya taka da karfi,tsabar azaba batasan lokacin da tayi Kara ba,cikin sauri momma tace"lafiya kuwa?"

Suna hada idanu da haidar ya galla Mata harara da sauri tace"babu komai",murmushi momma tayi .

Suna komawa gida suka shirya domin tafiya kamar yadda sukazo haka suka tafi kowa a motarshi.

Farouk ya dauke hanyar kano su kuma suka wuce adai-dai Zaria sumayya ta koma motar haidar ya ja suka tafi,shi kuma farouk ya tafi gida.

Yau satin su daya da dawowa farouk yana zaune humaira ta shigo,kallo ya bita dashi,tab wannan za'a aura masa hmm! Da sake aradu😄.

Gefe ta nema ta zauna kallonshi tayi tace"yaya na kawo maka abinci,girgiza kai kawai yayi,shiru tayi tana wasa da yatsan hannunta.

Shi kuwa zuba Mata idanu yayi yana tunani,inna Mari tayi sallama ta shigo ,da murna tace"ga baffanku can ya dawo yace kuje"a tare suka mike suka tafi,

A zaune yana cin abinci,yana garinsu yayi murmushi yace"alhamdulillahi dazu mai martaba ya kirani yake gaya mini abin arziki.

Da mamaki farouk yace"me kenan?",Dan murmushi yayi yace"mai martaba ya biya mana hajji wannan Karan zamu sauke faralli.

Dariya farouk yayi yace"Allah ya sanya alkhairi zan kirashi na mishi godiya,shafa kanshi yayi yace"Allah ya muku albarka ga kanwarka nan Dan allah ka riketa amana.

Sunkuyarda kai yayi yace"insha Allah baffa dame zan saka muku irin abinda Kuka yi mini.

Baffa yace"kai dana ne farouk Dan haka duk abinda nayi maka sauke hakkine ,sannan insha allahu bazaka tabe a rayuwa ba iya biyayyar da kake mini ko Dan Dana haifa sai haka.

Shiru wajen yayi kafin baffa yace"kunci abincin?",girgiza kai farouk yayi,baffa ya kalli humaira yace kawowa farouk abinci mana.

Washegari da yamma farouk ya shigo gidan waya a kunnenshi da alama waya yake yi.

Humaira dake wanki ta amasa sallamarshi ta cigaba da wankinta daga nesa ya ya tsaya

yace"haba salim idan kayi wani abin sai kace yaro karami haba yaushe muka rabune.

Sallama momma tayi ta shigo,da mamaki farouk ya kalleta human kuwa da gudu taje ta rungumeta,shafa kanta tayi tace"anata wanki ne"daga kai kawai tayi.

Farouk ta kalla tayi mishi alama da yazo,murmushi yayi sannan ya matso kusa da ita,cikin sauri ta rungumoshi,wanda yayi dai-dai da fitowar inna Mari.
Momma cikeda kunya ta sake shi,inna Mari kuwa yi tayi kamar bata gansu ba.

Washe baki tayi tana musu sannu da zuwa,karasawa tayi,bayan sun gaisa sannan inna Mari tace"bari a Kira baffan.

Bayan farouk ya Kira baffan,yana shigowa ya ganta shima cikin murna ya Mata sannu da zuwa.

A varender suka zauna,humaira ta kawo Mata ruwa da drinks,murmushi tayi tace"sannu da aiki".

Bayan Tasha ta kalli baffa tace"abinda ya kawo ni nan shine naji ance mai martaba ya biya muku aikin hajji,to shine nace mai zai hana kuyi parking ku koma gidanku idan yaso sai ayi biki kunacan"

Murmushi baffa yayi yace"hajiya banki ta taki ba sai dai inaso ya kasance bikin farouk a kano za'ayi shi zai zama zamu je mu amso mishi auren hunaira a wajen yan uwana idan akayi haka sai washe gari a wuce adamawa",

Shiru momma tayi na Dan lokaci kafin tace"shikenan hakan ma yayi,idan Allah ya kaimu bayan biki sai Ku koma"

Inna Mari tace"ni aganina mai zai hana idan mun dawo saudiyya sai mu sauka acan"

Baffa yace"kwarai kuwa kin kawo shawara mai kyau hakan za'ayi".

Momma tace"to bayan wannan inaso idan babu damuwa a bani amarya na tafi da ita"baffa yayi dariya yace"wannan kuma keda yar ki amma ni ango yana nan.

Dariya itama momma tayi kafin ta kwalawa humaira Kira,cikin sauri humaira ta fito,momma tayi murmushi tace"dauko hijab mu wuce ko.

Humaira ta Amsa sa to,sai da ta Kara gyara fuskarta sannan ta dauko hijab din.

Inna hadiza tace"aifa dama akuyar daure ta sami sake babu tamabayar ina za'a je babu komai.

Humaira ta rufe fucks tace"ai nasan momma bazata kaini inda zan cutu ba.

Kowa na wajen yaji dadin maganar data gaya,farouk kuwa ji yayi kamar ya janyota ya rungumeta,momma ta kalli inna hadiza tace"to kinji ko?

Har bakin mota farouk ya rakasu,momma ta kalli farouk tace"to sai bayan an daura aure ko?" Shafa kanshi yayi yace"momma!.

Kudi ta ciro ta mika mishi tace"gashi ka rike wannan a hannunka,sati mai zuwa zan aiko maka da sako"murmushi yayi yace"to momma Allah ya kiyaye hanya,ta Amsa da ameen,shigewa Mota tayi ta barsu domin suyi sallama.

Shiru wajen yayi,ahankali humaira ta dago,idanunshi na kanta hakan yasa idanun nasu haduwa,a lokaci daya zuciyarsu ta buga,tunda aka sa musu rana yaune ranar da suka tsaya cikin kwanciyar hankali suka kalli juna.

Momma ganin kallon  yaki karewa yasa tayi musu horn,cikin sauri farouk ya zare nashi idanun ya maida kan momma,da hannu tayi mishi alamar lokaci.

Humaira kuwa sunkuyar da kai tayi tana wasa da yatsun hannunta ita kadai tasan me take ji azuciyarta.

Farouk cikin dashewar murya yace"yanzu ya za'a yi mu dinga magana ko shikenan,girgiza kai tayi tace"ka kira ata momma kawai.

Murmushi yayi yace"to shikenan amma ai bazan dinga ganinki ba,kasa tayi da kai tace"za kayi missing dina ne?,waro idanu yayi yace"kefa?"daga kai tayi tace"sosai ma,
Lumshe idanu kawai yayi zuciyarshi na bugawa.

Momma ta Leko tace"ko na tafi na barku ne, da sauri humaira ta nufi motar,har ta bude murfin kofar ta tsaya da sauri ta juyo tace"kai fa baka bani amsa ba.

Ido cikin ido ya kalleta yace"zanyi fiye da yadda kike tunani,murmushi ta saki shima haka ya daga Mata hannu alamar bye.shiga tayi ta maida murfin ta rufe,momma tayi murmushi taja motar.

Nidai nace"hmm su farouk an iya soyayya babu ko kunyar momma😂

One love😘 taku ce ❤

*📑FAROUK KO  HAIDAR* 📑

*~GOLDEN PEN WRITERS ASSOCIATON~💫💫💫*

https://www.facebook.com/groups/1569379426621615/

*~❄we beare's of soon golden we writer's assiduously percieven No pain so magical Our creative golden pen Be hold our worlds A production of our pen savour Out worlds for it cause u np pain~*

Written 🖊by deeja one love

Dedicated madina m umar🌹

56-57

Direct Zaria suka wuce,mama ta taresu cikin farin ciki,humaira kuwa wajensu husna ta wuce.

Suna zaune salim ya shigo,cikin murna yace"oyoyo momma zuwa babu sanarwa,kallon humaira yayi yace"momma kin biya kano ne?"

Daga kai tayi,cikin sauri yace"kin taho da farouk ne?"mama tace"ikon Allah farouk din yarone da sai ta taho dashi.

Dariya sukayi duka,tabe fuska salim yayi yace"to ai nasan zai biyo ta ne,mama tace"ya biyo ta yayi me?turo baki yayi yace"yazo wajena.

Rike haba mama tayi,momma kuwa murmushi kawai tayi,mama tace"to ai kai kasan inda yake sai kaje,Kara turo baki yayi yace"ba abba ya hanani ba".

Dariya ma ya basu duka,momma ta rike hannunshi tace nan da sati both ne fa zaku hadu a adamawa fa,Sosa kai kawai yayi.

Washe gari momma tace"dama fa Nazi tafiya da amare ne domin su zauna acan.

Abba yace"to ai babu matsala,ya kalli su husna yace"to ai sai Ku Tashi Ku shirya,humaira kuwa murna takeyi za'a tafi dasu.

Daganan kaduna suka wuce,basu sami  kowa a gidan ba sai surayya,tayi Murray ganinsu sosai.

Momma tace"ina mamien taking?",surayya tace"tana wajen aiki"momma ta kuma tambayarta ina haidar fa tace"yana hospital tare da daddy.

Daki surayya ta kai momma tayi sallah sannan ta kwanta kasancewar batazo da kowa ba duka a taraba ta bar yaran.

Sai shida mamie ta dawo,ganin momma tace"au ashe da baki a gidan,murmushi kawai momma

tayi.

Haidar kuwa sai bayan magrib ya shigo da murna ya matsa kusa da its yace"dazu ai salim ya kirani ya gaya mini kinzo,hannunshi ta rike tace"eh da yau naso na koma amma ban same Ku ba yanzu dole sai dai gobe.

Kanshi ya dora a kafadarta yace"shikenan hakan yayi ai.

Washe gari da wuri suka shirya,shima har parking lot ya kawota momma ta ciro kudi ta bashi tace"sati mai zuwa za'a kawo muku sako in allah ya yarda.

Mota ta shiga ta barsu domin suyi sallama,gefe ya kalla ita kuma ta cigaba da Danna wayarta,ganin shirun yayi yawa yasa ta dago ta kalleshi.

Dan tabe baki tayi ta juya ta fara Tasia,hannunta  ya rike a hankali yace"Allah ya kiyaye hanya,da sauri ta kalleshi kamar bashi yayi maganar ba Dan ko kallonta be yi ba,a sanyaye tace"ameen.

Be saki hannun ba haka ita ma bata kwace ba,sunfi five minutes a haka Sannan ya saketa a hankali,cikin sauri ta tafi har ta bude kofa sannan ta juyo ta kalleshi ,shima ita yake kallo,murmushi yayi ya juyar da kai,itama murmushin tayi sannan ta shiga.

Tana shiga yusra ta kalle ta tace munafikai kuna so kuna kaiwa kasuwa,harararta surayya tayi tace"ke kuma kina sa ido ko?,dariya sukayi,itadai momma batace komai ba.

Farouk ya kira mai martaba yana dagawa yace" abokina  ya dai"?,murmushi farouk yayi sannan ya gaisheshi,yace"mai martaba dama na Kira ne nayi godiya".

Mai martaba yace"tame fa?farouk yace"baffa yace ka biya musu saudiyy........'cikin sauri mai martaba yace"ya isa haka Dan na yiwa su baffanka abu bai zama dole ka Kira kayi godiya ba,umar ina son mahaifinka da mahaifiyarka sosai su kuma suna sonka,,,dole ne naso abinda suke so ko?Dan na cika masoyin gaskiya😁,abin dariya ya bawa farouk.

Yusra tayi dariya tace"ai wallahi soyayyar Ku humaira akwai burgewa ni na kalla kun fi kowa kyau ne,dariya aka kwashe dashi.

Kallon su tayi tace"nifa da matsala,cikin sauri suka ce"meye matsalar?,nan ta kwashe komai ta basu labari.

Shiru suka yi kafin sumayya tace"amma kin bani mamaki wallahi yaushe ake haka sai kace zamanin da kinfa yi makarantar boko bare ace gidadanci ke Damon ki,husna ta amshe da cewa"ki zauna wasa wallahi zaki ga wasa duk zurfin cikin yaya farouk har ya iya fitowa ya gaya miki amma ki kasa ganewa bari ya miki kshiya naga ta tsiya.

Yusra tace"to bude kunnuwan ki kiji wallahi kodai ki gyara ko a gyareki tab su fa maza sun fi so suga mace wayayyiya amma kin zauna kauyenci,ita dai surayya bata ce komai ba.

Fada suka yi Mata sosai da sosai sannan suka koma labarin honey moon,yusra tace"wai kuna ta shirye-shirye ko?.

Husna tace"Sosai ma gobe zamuje passport,yusra ta dubi surayya tace"ke wai me Zaku je yi?,banza surayya tayi da ita.

Sumayya kam harara ta gallawa humaira kafin tace"ga wannan vanzar da taja mana nan,wai my choco idan yaya farouk baza suje ba muma haka,dariya akayi gaba daya.

Humaira tace"aikuwa kun lashe,marairaicewa sumayya tayi tace"Dan allah ki taimaka ki lallaba Mijin ki yayi mishi magana muje tunda Ku ba zuwa Zaku yi.

Meye tukuici na"humaira tace,sumayya tace"wallahi a ranar da zamu bar kasar nan zan baki",to shikenan.

*📑FAROUK KO  HAIDAR* 📑

*~GOLDEN PEN WRITERS ASSOCIATON~💫💫💫*

https://www.facebook.com/groups/1569379426621615/

*~❄we beare's of soon golden we writer's assiduously percieven No pain so magical Our creative golden pen Be hold our worlds A production of our pen savour Out worlds for it cause u np pain~*

written🖊️ By Deeja One Love

Dedicated to madeena m umar🌹

Sister feenerh ina tayaki murnar gama littafinki mai suna auren soja allah ya Kara hade kanmu ameen

Wannan page din sadaukarwa ne ga duk mai suna umar farouk.

Sannan wajen numbering ina mistake kuyi hakuri,
bubuwa ne sun fara mini yawa abinka da mai Iyali lols,
Sorry for my mistakes.
65-66

Sai da sukayi isha sannan kowa ya zo ya dauki matar shi.

Suna komawa farouk wanka kawai yayi ya kwanta,humaira kuwa ta dade tana tunanin magan-ganun dasu yusra suka gaya Mata.

A sanyaye ta shigo dakin ganin ya kwanta ya sata ajiyar zuciya,wanka tayi ta canja kaya sannan ta kwanta.

A hankali take bin fuskarshi da kallo maganar yusra ke dawo mata inda take cewa"ko be neme ki ba ke ki neme shi,jinjia kai kawai tayi yama za'ayi ta iya wannan ai rashin kunya ne.

Hannu tasa ta shafa daga kan hancin shi har wajen bakin shi,cikin shagwaba tace"my icy i love you to amma taya wai zan kawo maka kaina bayan kai baka nema ba,rufe idanu tayi wai ita taji kunya.

Light kiss tayi mishi a goshi sannan ta kwanta akan kirjin shi a haka har barci ya dauketa.

Farouk ya shafi inda tayi kissing dinshi cikin tsananin murna yace"love you too my teddy",
Cikin shauki yau suka kwana.

Yau dai masu honey moon suka daga zuwa kasar oman,washe gari kuma farouk ya fara aiki a hospital din su.

Farouk ya shigo gida a gajiye,cikin sauri humaira ta tarbe shi,orange juice mai sanyi ta tare shi da shi.

Kallon shi tayi tace"yaya farouk wanka,a gajiye yace"teddy kiyi hakuri na gaji",cuno baki tayi.

A hankali ya mike ya shiga wankan,kayan shan iska ta ciro mishi,white three quarter da light pink armless.

Murmushi yayi domin tana wajen kula dashi humaira bata wasa sai dai kuma ta kasa biya mishi bukata har yanzu.

A kan dinning ya sameta,abinci yaci sosai domin kuwa cous cous tayi daya ji vegetables.

Bayan kwana biyu,humaira ta fito a zaune ta sami farouk yana waya da salim,kan kafar shi ta zauna,lumshe idanu yayi yace"da gaske".

Bata ji me salim din yace ba,farouk cikin farin ciki yace"to yaushe zaku wuce india?,nan ma bata ji me salim yace ba,farouk ya kuma cewa"ok allah ya kaimu,zan sa ran ganin Ku nan da sati biyu idan kuka wuce ko,to kada ka nufo adamawa kaji na gaya maka,dariya yayi sannan ya kashe wayar.

Sakala hannun ta tayi ta wuyan shi tace"me yaya salim yake gaya maka",Kara janta jikin shi yayi yace"sumayya is three weeks pregnant,dariya humaira tayi tace alhamdulillahi kai amma naji dadi wallahi.

Shinshina wuyanta yayi yace"ke yaushe zaki bani baby,murmushi kawai tayi.

Hancin su ya goga yace"ki shirya mana kaya gobe zamu wuce taraba",cikin murna tace Allah ya kaimu.

Washe gari da safe humaira ta Kira sumayya ta Mata ya jiki,sumayya tace"yadai komai. ya kankama kuwa?"humaira ta amsa da"na kasa wallahi",sumayya tace"ya kinyi amfani da turaren da na baki kafin na tafi?"Humaira ta kuma amsawa da"a'a.

Murmushi sumayya tayi tace"to ki saka a jaka sannan ki tabbatar da idan kunje kin sa sannan da dare fa",tsaki humaira tayi tace"insha allah zan yi amma shi turaren har wani doka yake

da?,dariya kawai sumayya tayi tace"ki Kira yusra itama kiyi Mata ya jiki domin itama nata two weeks ne.

Dariya humaira tayi tace"wato ku daga zuwa honey moon an samo yan oman kenan",sumayya tayi dariya tace"kedai ki zauna neman duniya,kinji sai anjima habiby na jirana,kan humaira tayi wata magana har sumayya ta kashe wayar.

Kiran yusra tayi itama tayi Mata ya jiki,nan dai itama ta tambaye ta itama nan dai ta bata shawarwari.

Tana kashe wayar farouk ya shigo,kallon ta yayi yace"gulmar waye kuke yi?"girgiza kai tayi tace"a'a wallahi da aunty yusra ne itama ya jiki nayi Mata.

Murnushi yayi yace"zo muje idan kin gama inaso mu isa da wuri.

Sai da suka biya gidan mai martaba sannan suka wuce.

Ana kiran sallar azahar suka isa Dan haka farouk yana sauke ta ya wuce masallaci.

Momma tayi farin ciki sosai,bangaren da idan sunzo suke zama momma ta bude musu,da Islam da ihsan sun girma sosai.

Kara kakkabe shi humaira tayi sannan ta zuba kayan su.

Da dare bayan sun yi dinner,nan suka zauna suka dinga fira,zuwa can humaira ta mike ta tafi ta kwanta.

Momma ta dubi farouk tace"babu wata matsala ko?",amsa ya bata da eh.

Bangaren humaira kuwa bayan tayi wanka tasa kaya har ta kwanta kawai turaren ya fado Mata arai,tashi tayi ta dauko tace"yau dai bari na sa naga mai zai faru,an tayowa tayi ta zuba a jikin ta,Dan danan dakin ya dau kamshi,sannan tajeta kwanta.

Farouk yana shigowa yaji dakin ya canza kamshi domin kamshin yayi dadi,bayi ya wuce sai da yayi wanka sannan ya sa kaya ya kwanta.

A hankali yaji numfashin shi na sarkewa,cikin sauri ya matsa kusa da ita,dandanan hankalinshi ya bar jikin shi,shafa ta yake yi kota ina.

Humaira cikin barci taji wani bakon yanayi,kafin ta gama bude idanu,tuni farouk yayi nisa.

Nidai daga nan nayi waje Dan maryam khamis(my one love)ta hanani bin kwakwaf da gulma.

08139698893

For your comments korafi ko shawara.

❤one love taku ce😘

*📑FAROUK KO  HAIDAR* 📑

*~GOLDEN PEN WRITERS ASSOCIATON~💫💫💫*

https://www.facebook.com/groups/1569379426621615/

*~❄we beare's of soon golden we writer's assiduously percieven No pain so magical Our creative golden pen Be hold our worlds A production of our pen savour Out worlds for it cause u np pain~*

written🖊️ By Deeja One Love

Dedicated to madina m umar🌹

67-68

Sai da hankalin shi ya dawo jikin shi sannan ya lura da barnar da yayi,humaira kuwa idanu yayi ja majina da hawaye sun hade gaba daya.

Shafa kanta yayi cikin sanyin murya yace"am sorry teddy hankali na ya gushe ne,banza humaira tayi dashi.

Ruwa ya. Tara mai dumi sannan yazo ya dauke ta ya saka a ciki,tun tana jin zafi har ta dawo tana jin dadin ruwan,sai da ya ga ta fara wankan tsarki sannan ya fita ya barta.

Gyara gadon yayi,humaira na fitowa yayi saurin tarar ta hannunta ya rike ya kaita ya zaunar da ita,wata rigar ya dauko ya sa Mata sannan ya kwantar da ita.

Yau wani iska yake ji tana kada shi me dadin gaske.

Sallaya ya shimfida sannan ya fara jero lafiloli yana godiya ga allah domin gaskiya yau ya sami nutsuwar daya jima be samu ba.

Sai da yayi alwala sannan yazo ya tayar da ita,hankali ta taka ta shiga bathroom din,ganin ta shige yasa farouk yayi murmushi ya fita.

Tana idar da sallah ta haye bed ta cigaba da barcin ta,koda farouk ya dawo be tada ita ba,qur'ani kawai ya bude ya fara karatun shi.

Sai karfe bakwai sannan ya tashi da falo ya fara sai da ya gyara shi tsaf sannan ya shiga

kitchen ya dora musu break fast.

Momma na fitowa ta fara jin kamshi,cikin mamaki ta fara fadin"humaira ba dai kece a kitchen ba",maganar ta makale ganin farouk daure da apron yana yanka albasa.

Dariya abin ya bata tace"farouk kai ne a kitchen?shafa kai yayi cikin jin kunya yace"eh momma,"rike haba tayi tace"ikon allah ina humairan?"shafa kanshi ya kuma yi yace"tana barci.

Jinjina kai kawai tayi,anan ta zauna suna fira yana aikin.

Sai da ta gama sannan ya wuce part din su,humaira ya samu ta fito wanka kenan,suna hada idanu tayi saurin saukar da nata domin wani kunya taji.

Murmushi yayi yace"yau kuma kunya ta kike yi,shiru tayi hannunta ya rike yana murzawa a hankali.

Humaira jin tsigar jikin ta na tashi yasa tayi saurin dago idanu tana kallonshi,sunfi thirty second suna kallon juna sannan tayi saurin janye nata idanun,a hankali ta furta"ina kwana.

Kwankwason ta ya riko ya jingina ta da jikin shi,peck ya Mata a goshi yace"lafiya lau,ya gajiyar jiya?"

Fuskarta ta boye a jikin shi tana murmushi,shima murmushin yayi ya rungumeta sosai.

A hankali ta zame jikin ta daga nashi ta wuce dressing mirror,shikuma farouk wardrobe ya bude ya zabo Mata kaya.

Wata jar atamfa me ratsin blue sai alkyabba blue,tayi kyau sosai,murmushi tayi wato Mijin ta akwai shi da son blue colour.

Hannunta ya rike yace"kinyi kyau,muje muyi break fast,"murmushi kawai tayi.

A dinning suka sami mutanen gidan,gaishe dasu tayi sannan ya ja Mata chair ta zauna.

Baby tayi serving din su,tana cin abincin ta dago hada idanu suka yi murmushi yayi ya kashe Mata ido daya,murmushi itama tayi tana juyawa suka hada ido da momma,tashi momma tayi kawai tana murmushi.

Suna gama cin abincin ya nada Mata mayafin alkyabbar yaja hannun ta suka bar gidan,wani garden suka je nan suka kusa wuni sai idan lokacin sallah yayi suke zuwa suyi,zallar love kawai take gani,har mamaki abin yake bata.

Da yamma suka baro wajen,a super market suka tsaya nan tayi siyayya sosai sannan yaja hannun ta suka fice.

A mota ta kalle shi tace"yanzu yaya me zan cewa momma idan mun koma",dariya yayi yace"kice mata kin fita da Mijin ki ne",shiru kawai tayi.

Suna komawa gida momma bata ce musu komai ba,tana shiga part din su ta kira sumayya tana dagawa tace"allah ya isa wallahi",dariya sumayya ta kwashe da ita tace"yaya farouk ya kashe arna jiya kenan",humaira tace"hmm har da munafikai Dan wallahi nasha wuya,nan dai sumayya tace"ki Kira yusra zata baki wasu sirrakan.

Kwanansu uku suka koma adamawa,yanzu humaira an fara sanin dadin miji,kuma ta Kara haske.

Humaira ta kalli agogo yanzu duk inda farouk yake ya kusa dawowa,tashi tayi ta shiga wanka,wata riga ta saka iya cinya transparent komai ana gani rigar baby colour,ana iya hango blue pant din ta.head band blue ta saka simple make up ne a fuskarta.

Bathroom ta shiga ta tara mishi ruwa sannan ta dawo falo fridge ta bude ta dauko hadadden kunun ayan ta,tana ajiyewa taji tsayuwar motar shi.

Kafin tazo bakin kofa har ya danna door bell,cikin sauri ta bude kofar,murmushi suka aikawa juna kafin tayi peck din shi a goshi.

Hannun shi ta rike ta kai shi har bed room,takalman shi ta fara cirewa sannan belt riga sai wando,towel ta dauko ta mika mishi,murmushi yayi ya daga ta cak yayi bayin da ita,cikin bathtub ya jefa.

Humaira tayi ajiyar zuciya sannan ta tabe fuska,dariya ya farayi wanda yasa humaira zuba mishi idanu,tsayar da dariyar yayi sannan ya daga Mata girl daya alamar lafiya.

Hade fuska tayi hawaye ya zubo mata,cikin sauri ya shigo cikin ruwan ya fara tambayarta lafiya,baki ta tabe tace"na maka kwalliya baka gani ba ka bata mini.

Hannun shi ya saka cikin rigar ta yace"ganin dana yi ne na yaba yasa nake so na bata kwalliyar,kan tayi magana ya hade bakin su.

Fita waje nayi domin jiransu.

Bayan wani lokaci suka fito dukkansu daure da towel white jeans da blue shirt suka saka.

Har falo ta kaishi sannan ta zuba mishi kunun ayar yana sha yana santi,ita kuma sai dariya take yi mishi ya kuwa sha da yawa.

Janyota yayi ya zaunar da ita kan jikin shi sannan ya ciro wayar shi yayi musu selfie.

Hannun shi ya Dora kan cikin ta yace"ranar Monday zaki fara attending lectures a( futy),cikin murna tace"na gode sosai my peach.

Yau humaira ta fara attending lectures a gajiye ta dawo,tana shigowa tayi wanka ta dora abinci.

Da yamma farouk ya dawo,cikin murna ta tarbo shi bayan sunyi wanka yace Mata"zo muje kiga surprise.

Mota ya siya Mata new model yar karama bata san lokacin data rungumeshi ba,cikin tsananin murna tace"na gode mijina allah ya barmu tare",da sauri ya karasa Mata"yasa na Miki kishiya",hannu ta kai ta bugi kirjin shi,hannun ya rike yace"wane ni matukar kina bani farin ciki baki ba kishiya,hade bakin su tayi tana aika mishi wasu sakonni.

❤❤❤❤❤one love ❤❤❤❤❤

*📑FAROUK KO  HAIDAR* 📑

*~GOLDEN PEN WRITERS ASSOCIATON~💫💫💫*

https://www.facebook.com/groups/1569379426621615/

*~❄we beare's of soon golden we writer's assiduously percieven No pain so magical Our creative golden pen Be hold our worlds A production of our pen savour Out worlds for it cause u np pain~*

written🖊️ By Deeja One Love

Dedicated to madina m umar🌹

Wallahi big bro i don tired😖

69-70

Yau satin yan honey moon daya da dawowa,humaira ta Kira su ta musu sannu da zuwa domin

makaranta bata samin lokacin zama,suma su haidar a yau suka fara zuwa wajen aikin.

Farouk yana shigowa ya sami humaira na waya,kwanciya yayi ya dora kan shi akan kafar ta,ganin wayar taki karewa ya sashi saka hannu a cikin rigar ta,dole yasa tayi sallama da sumayya.

Farouk kuwa yana ganin ta kashe wayar ya hade bakin su,sai da yayi kissing dinta yadda yake so sannan ya hakura.

Lumshe idanu yayi yace"Dawa kike ways?",shafa fuskar shi tayi tace"da sumayya ne tana gaya mini wai gobe tun da bani da lectures mu hadu a gidan yusra.

Be ce komai ba ya mike ya shige bedroom,da idanu ta bishi a ranta tace"me hali baya fasawa,mikewa tayi tabi bayan shi.

A kwance ta same shi,kwanciya tayi a jikin shi tace"my peach ko kada naje ne",idanun shi a lumshe yace"ni na isa mijin ki sumayya ta baki umarni",da sauri tace"bafa haka bane wata fassarar kayi kaga tunda suka dawo bamu hadu ba shiyasa",shiru yayi bece komai ba.

Washe gari humaira har ta cire rai da zuwa,tana zaune tana yanke farce,farouk ya amshi nailcutter din ya cigaba da yanke mata,tace"haba peach ka tafi wajen aiki mana idan yaso na yanke.

Shiru yayi bece komai ba,sai da ya gama yanke mata sannan yace"kin fasa zuwa kenan?",da mamaki tace"ai naga baka yarda ba",da sauri yace"jeki shirya,da sauri ta mike.

A bakin get ya ajiye ta sannan ya juya ya tafi,cikin sauri ta karasa gidan,da murna suka tare ta.

Bayan sun gaisa,yusra tace"gayan sirrin ni naga sai kyau kike karawa ne"dariya akayi kafin humaira tace"ni da nazo ki bani wasu sirrikan,dariya suka kuma fashewa dashi.

Yusra tace"sirrika kinzo gidan su,nan ta fara zayyanowa.

1
Ki sami sassaken baure da kanumfari ki tafasa su idan ya tafasu sai ki tace ki saka mazarkwaila idan ya wuce ki dinga sha.

2

Ki nemi kankanar ki da dabino ki bare dabinon ki sai ki wanke,kankanar kuma sai ki fafe samanta ki debi dabinon ki zuba a ciki,ki barshi ya kwana sai ki kwashe dabinon ki cinye kankanar ma haka ki hada harda 'ya'yan.

3
Ki sami dabinon ki da zuma ki bare dabinon ki wanke sai ki zuba su a cikin zuman,ki rufe idan ya jiku ki cinye duka harda zumar.

4
Ki nemi kankana,cucumber,dabino,tumatir ki hada kiyi blanding din shi ki tace kina sha.

5
Ki sami zogale ki shanya idan ya bushe ki daka idan yayi laushi ki zuba madara peak ki shanye.

Surayya ta Kara da cewa"

Ki dimanci yawan shan abu mai ruwa irin su fate dadai sauran su.

Sannan ki dena zama babu dankwali ko kina taka tiles babu takalmi ko zama akan shi,ki yawaita yin lallen gargajiya kina rage saka mayafi koda yaushe ki dinga rufe jikin ki.

Banda tsarki da ruwan sanyi haka kuma kada ki yawaita shan ruwan zanyi,ki yawaita shan fruit sannan shima zaki iya bashi yana sha,zogale rama cocumver,tomato,rake, ki dinga cin su.

Kullum kan ki kwanta ki dinga saka kanumfari guda daya a bakin ki kina tsotsa.

Ki sami habbatus sauda ki tafasa idan kika sauke ki barta ta huce sai ki tace wanda ya kwanta a kasa ki shanye,sai kina tsarki da wanda kika tace.

Duka idanu suka zuba mata suna mamaki,yusra tace"yaushe masu girman kai suka sauko?",dariya tayi tace"ai mu a aikace muke nuna soyayyar mu kune kuke wani fade a baki",dariya akayi duka.

Sumayya tace"Sannan akwai wata yar maiduguri da take zuwa wajen fulani na sami number din ta har mun yi waya idan kuna so turarrurruka take siyarwa nace ta kawo mini,idan kuna so to zan sa ta kawo mana gaba daya,a dinga hadawa da kamshi kuma.

Husna tace"hakane amma duk da haka sai mun hada da hakuri Dan wallahi duk kisisina da shan magane-magane bashi bane,zaman ya wuce wasa dole wata rana ku sami sabani Dan haka ke mace kece a kasan shi sai kin yi hakuri fiye da nashi,kada ki dauki wai daga kin iya kissa da kisisina da kuma shan magani shikenan auren ki ya gyaru,ayya sister dole ki aro hakuri ko baki dashi ki yafa akan ki allah yasa mu dace ameen.

Tabbas abinda husna  ta fada gaskiya ne,kuma su kansu sun yarda da abinda ta gaya.

Sai da yamma sannan kowacce mijinta yazo ya dauke ta.

Washe gari kuwa humaira ta fara gwadawa,ita kanta tasan ta canza domin yadda take jin kanta.

Da yamma farouk ya dawo,kamar yadda ta saba haka ta tare shi bayan sun gama komai farouk yace"teddy me kika sha ne?",girgiza kai tayi tace"meya faru",naji kinfi sweet din lollipop dadi ne",dariya tayi tana rufe bakin ta.

Yanzu humaira karatu ya fara zafi yau suka gama tests din su zuwa sati mai zuwa zasu fara exams end of third semester.

Cikin yusra da sumayya wata shida takwas kenan surayya da husna kuma Wata hudu,humaira

ce kawai single.

A gajiye yau ta dawo wanka kawai tayi ta kwanta domin anjima tanaso ta tashi tayi karatu gashi tasan mijin ta bazai barta ba,shafa cikin ta tayi taji lakwas alamar yunwa takeji,daga haka barci ya dauke ta.

❤❤❤one love fa guys and babes❤❤❤.

*📑FAROUK KO HAIDAR* 📑

*~GOLDEN PEN WRITERS ASSOCIATON~💫💫💫*

https://www.facebook.com/groups/1569379426621615/

*~❄we beare's of soon golden we writer's assiduously percieven No pain so magical Our creative golden pen Be hold our worlds A production of our pen savour Out worlds for it cause u np pain~*

written🖊️ By Deeja One Love

Dedicated to Madeena m umar🌹

Ummee yusuf ina taya ki murnar gama littafin ki mai suna"ukubar kishiyata"allah yasa kifi haka ameen

A page daya wuce nayi mistake ba habbatus sauda ba hulba nake so nasa sai ku kiyaye,na gode.
71-72

A hankali yake shafa fuskarta,bude idanu tayi sannan tayi mika,murmushi tayi masa tace"peach

ka dawo?",hannun ta ya rike ya mikar da ita,bathroom ya kai ta kamar teddy haka ya Mata wanka ya fito da ita,da kan shi ya shafa mata mai ya canza kaya .

Hannun ta ya rike yace"muje mu ci abinci",komai anyi settling akan dinning kujera ya Mata yace"zauna,lafiyayyen jalop din shinkafa ne wacce taji vegetables sai farfesun kifi,a baki ya dinga bata har ta koshi,sannan yaci shima.

Idanu kawai ta zuba masa tana kallon shi,"daga mata gira yayi alamar lafiya,murmushi tayi tace"wato baffa ya gama mini komai a duniya,bayan ya iganta rayuwa ta sannan dana kai minzalin aure ya hada ni da gwarzon namiji wanda zai kula dani,wanda zai sadaukar da farin cikin sa Dan nawa,ya bata lokacin sa dan ya faranta mini rai,INA SON KA FAROUK da ban aure ka ba da ban San ya rayuwa ta zata kasace ba.

Hannun ta ya rike yace"humaira ni ya kamata nayi godiya wa baffa domin tun ina karami dai dai da rana daya ban taba ganin abinda zai sa inji a raina ni ba dan gidan bane,hasalima soyayyar daya ke mini tafi ta duk sauran yaran shi,kun San da hakan amma baku taba kishi Dani ba karshe ma taya shi kuka yi,bayan na girma ya dauko 'yar shi guda daya daya haifa ya bani ita aure,me zan cewa baffa,wallahi humaira koda bana son ki bazan iya wulakanta ki ba ballantana ma kece CIKAR MURADINA YAR UWATA.

Rungume shi tayi tana mai jin farin ciki.

Yau su baffa suka tafi saudia domin sauke faralli,haka a lokacin allah yayi wa hajiya salma rasuwa,abin gwanin ban tausayi,domin yaran ta sun shiga tashin hankali har gwara ammar yakan danne ya nuna babu komai amma uwa uwace ko yaya take.

Bayan anyi bakwai kowa ya koma inda yake,a lokacin humaira ta fara jarabawa,tun daga lokacin farouk ya dauke Mata aiki indai ba Tana da interval ba.

Koda yaushe tayi magana sai yace"humaira tun kina karama nake da burin kiyi karatu yanzu dama ta zo Dan haka kiyi amfani da ita kan ta wuce (damar da yawancin matan hausawa ke wasa da ita kenan,mijin ki ya barki karatu kiyi ta shiririta,duk da yanzu naga babu laifi ana gyarawa allah ya Kara fahimtar damu ameen.)

Suna gama jarabawa ya dauke ta suka tafi fada,bayan sun gaida mai martaba suka wuce taraba kwana biyu kawai suka yi suka wuce kaduna,sai da suka yi sati daya sannan suka dawo.

Bayan kwana biyu ya kaita gidan salim,sun yi farin cikin ganin juna,sumayya anyi nauyi haihuwa yau ko gobe.

Sumayya tayi murmushi tace"humaira dan allah kiyi wa yaya farouk magana yayi mishi magana ina so ya kai ni kaduna na haihu acan,murmushi humaira tayi tace "haba kada ki damu kinji consider it done",Cikin farin ciki suka rabu da juna.

Da dare suna kwance humaira tace"yauwa peach sumayya ta bani sako tace Dan allah kasa baki,shiru yayi bece komai ba,cuno baki tayi tace"peach ina magana fa",still bece komai ba.

Mutsikka idanu ta fara yi alamar zata yi kuka da idanu ya bita kafin ya janyo ta jikin shi hannu ya kai ya dauko wayar shi dake ajiye a bed side cabinet.

Number din salim ya nemo ringing daya ya daga,cikin sauri yace"lafiya Dan uwa",murmushi yayi yace"kabar sumayya taje kaduna ta haihu acan mana,"shiru yayi kafin yace"to shikenan bro zan kai ta gobe in allah ya yarda",suna kashe wayar ya janyo humaira jikin shi yace"shikenan ai ko?,daga kai tayi.

Washe gari ya dauke ta ya kaita aka Mata passport,a kwana biyu da yake da kudi aka sama musu visa.

Salim ya kai su airport,suka wuce italy.

Kwanan su hudu a can sumayya ta haihu,murna kamar humaira tayi tsuntsuwa ta dawo,kullum ita kenan video call ana nuna Mata yarinyar ta.

Haka ranar suna through out tana online suna video call tana ganin yadda abubuwa ke tafiya.

Satin su biyu a can suka wuce Dubai sosai kasar ta burge humaira,soyayya kawai suke sha abin su.

Yana shigowa ya samu tana waya jan ta jikin shi yayi ya fara shinshinar wuyan ta,cikin sauri tayi sallama ta kashe wayar,bata fuska tayi tace"peach waya fa nake",bece Mata komai ba ya cigaba da abinda yake yi.

Hannun shi ta rike tace"kasan me da surayya muka yi waya tace wai taji kai ka yiwa salim magana ya bar ta taje kaduna ta haihu shine take so ka yiwa yaya haidar magana itama ya bar ta.

Shiru yayi kafin yace"humaira salim da haidar da bambanci,amma zan gwada na gani.

Wayar shi ya dauka ya Kira haidar din ringing daya ya dauka bayan sun gaisa yace"haidar me zai Hana itama ka taimaka ka barta ta je kaduna ta haihu mana",haidar yace'saboda me?,kai kana can kana honeymoon ni kuma ka barni gauro bazai yiwu ba",kafin farouk yace wani abu haidar ya kashe wayar.

Kallon humaira  yayi yace"ki bata hakuri tayi zaman ta kinji?,a sanyaye tace"to.

Yau saura kwana biyu su wuce India,kwance humaira take tana barci,farouk ya shigo kusa da ita ya kwanta,bude idanu tayi tace"ka dawo?,Kara shigewa jikin ta yayi.

Tudun da yaji cikin ta yayi ne yasa shi kallon ta,cikin sauri ya yaye blanket din data Rufa,bude idanun ta tabe fuska tayi tace"haba peach barci fa nake yi.

Da sauri yace"teddy when last kika ga period din ki?,shiru tayi tana tunani can tace"to ai kamar tun muna second semester wajen four month kenan,cikin farin ciki ya rungume ta yace"me yasa ban fahimci kina da ciki ba sai yanzu,saurin kallon shi tayi tace"peach ciki kuma?",daga Mata kai yayi yace"eh mana.

Washe gari suka tafi india a can ya kai ta hospital nan aka tabbatar mishi da tana da ciki har ma four month likitan yayi ta mamaki jin cewa farouk din shima likita ne amma wai be fahimta ba,sai da yace mishi"ita fa bata laulayi haka bega wani symptoms na pregnant ba sai jiya duk da dai ya kan lura da wani lokacin tana yawan barci.

Ai suna dawowa ya Kira salim cikin murna yace"salim humaira nada ciki har wata hudu",zaro idanu yayi yace"da gaske amma dama ranar da kuka zo ban gaya maka kamar tana da ciki ba ka musan ta,ai kuwa yanzu Labari zai bazu,suna ajiye waya salim ya fara yayadawa humaira nada ciki.

Kafin dare humaira gajiya tayi da daga wayar masu yi musu barka,sai farouk ne ya cigaba da dagawa,momma na Kira tace"amma nan zaka dawo da ita ta haihu ko,"shiru yayi,momma ta kuma cewa"farouk da kai nake fa,"farouk yace"momma kin ga ana strike ka Mata yayi ace yanzu ne muka mori hutun mu kan a koma.

Murmushi momma tayi tace"farouk kuka yi me,"da sauri ya kashe wayar.

Washe gari sai ga waya surayya da husna sun haihu,murna ba'a magana,duka maza suka haifa,ranar suna haka humaira taji kamar ta dawo.

Daddy hamma ya dinga Mata dariya,kuka ta sawa farouk akan ita ta gaji gida ta ke son dawowa,momma kuwa koda yaushe cikin kiran shi take kan ya dawo da ita.

Watan su biyu sannan cikin humaira wata shida suka wuce umara Dan su baffa tuni sun yi aikin hajjin su sun koma.

Humaira tayi farin ciki da ziyartar gari mai daraja garin madina,makka kuwa gata ga ka'aba abinda bata taba kawowa a ranta ba,ibada tayi ta sosai da sosai.

Sai da su kayi wata daya wai sai taga gari,karshe dai momma data gaji ta Kira salim ta gaya mishi.

Dawowar su daga da'if kenan wayar salim ta shigo,bayan sun gaisa salim yace"bro Dan allah Ku dawo haka wallahi nayi missing din ka sa yawa sannan momma tana ta kira na a waya wai na maka magana".

Farouk yayi murmushi yace"on friday jibi kenan zamu taho insha allah amma kada ka gayawa kowa,"cikin murna yace"babu wanda zan gayawa.

Washe gari ya kwashe ta suka je suka yi siyayya mai uban yawa,ranar friday jirgin su ya daga zuwa naija.....

Daga alkamin🖋️

One love

*📑FAROUK KO  HAIDAR* 📑

*~GOLDEN PEN WRITERS ASSOCIATON~💫💫💫*

https://www.facebook.com/groups/1569379426621615/

*~❄we beare's of soon golden we writer's assiduously percieven No pain so magical Our creative golden pen Be hold our worlds A production of our pen savour Out worlds for it cause u np pain~*

written🖊️ By Deeja One Love

Dedicated to madina m umar🌹

Sis nabeela allah ya baki lafiya yasa kaffara ne ameen.

73-74

Karfe biyu da rabi jirgin yayi landing a adamawa,salim ya Kira yace yazo ya dauke sure,sai da suka biya suka gaishe da mai martaba sannan suka wuce gida.

Haidar ya Kira a waya ya gaya mishi sun sauka,sauran dangi kuwa salim ne ya Kira su ya gaya musu.

Ita kam humaira a gajiya take,tun da tayi wanka ta kwanta bata Farka ba sai bayan la'asar,tana tashi ta rama sallolin da ake binta tukunna sannan ta fara neman abinci,a dinning taga babban leda tana budewa taga take away,murmushi tayi wato ya dawo kenan,tana gama ci ta koma komawa barcin ta.

Farouk na shigowa da mamaki ya ke kallon ta yace"wannan bata gajiya da barci ne.

Sai washe gari sannan su sumayya duka suka zo Mata sannu da zuwa,yusra tace"allah ke wannan irin kyau haka",amsar yarinyar dake hannun ta tayi tace"Kairat tayi girma(sunan hajiya salma aka sawa yarinyar),husna tace"ai yarinyar Kamar  ana Jan ta,dariya suka yi gaba d'aya.

Amsar ta hannun sumayya tayi tace"my takwara kin hadu,"dariya suka kwashe dashi haka suka cigaba da firar su har su haidar suka dawo daga wajen aiki.

Sai da aka kawo musu abinci,salim yace"bro amma kai ka girka ko?"murmushi yayi ya daga kai,haidar yace"shi yasa nace muku auren babbar mace yafi",faisal yace"wallahi yar shila tafi",haidar yace"ba wani yar shila ga mai hankalin da zata kula da kai",salim yace"to matan namu kenan su basu da hankali",nan fa husuma ta Tashi.

Farouk ya gallawa haidar harara yace"wai Ku baza Ku taba girma bane,anji kunya da yara da komai amma har yanzu kuna kuruciya".

Faisal yayi dariya yace"wallahi Ku gyara Dan zaku haifo yara yan wrestling,su dinga kwasan yan kallo.

Haka suka cigaba da firar su har suka kai bayan isha sannan kowanne ya dau matar shi suka wuce gida.

A yanzu haka cikin humaira ya shiga wata Tara,
Yau suka shirya zasu kaiwa momma ziyara
,kowa a motar shi zai dauki matar shi,farouk na gaba sai haidar sai salim.

Suna isa momma ta rin ka farin ciki haka ma inna Mari da inna hadiza domin sun same su acan.

Sai da suka gaishe da su sannan suka fita,ita dai humaira barci ta kwanta.

Da yamma duka suna falo,mazajen suka shigo,shirmen dai su haidar suke yi wanda baya kare musu.

Kusa da momma haidar yaje ya zauna,farouk kuwa humaira kawai ya nufi wajen ta,haka salim.

Sai da suka zauna suka huta sannan farouk yace"Ku tashi mu tafi kada dare yayi mana",momma tace"ban gane ba ina zaku farin?",salim yace"adamawa mana momma,"tace"to allah ya kiyaye hanya amma babu inda humaira za taje.

Da sauri farouk ya Kalle ta yace"haba momma ba muyi shirin barin ta ba fa",haidar yace"haba kai kuwa idan mun tafi da ita zata wahala sosai",farouk yace"gaskiya bazan iya barin ta ba haidar ta taso mu tafi kawai.

Inna hadiza da inna Mari babu wanda yace komai,
Momma ta numfasa tace"shikenan allah ta kiyaye hanya,har ta dauko hijab dinta,salim yace",ka bar ta mana kaji".

Kallon ta yayi yace"shikenan koma ki zauna na rinka zuwa",kowa sai da yayi mamaki,momma cikin dariya tace"gaskiya na kusa na fara kishi da kai salim,jifa nayi-nayi ya barta amma yaki,kai kana magana ya kyaleta,dariya akayi duka.

Haidar ya tabe baki yace"ai ni da nayi magana momma nima bai saurare ni ba",farouk yace"ai nima dana roke ka ka bar matar ka taje kaduna ta haihu kin barin ta kayi,salim kuwa ko tambaya ta dalili beyi ba ya bar ta",juyawa yayi ya kalli momma yace"kinga laifi na Dan nafi jin maganar salim?",girgiza kai tayi wato halin shi na riko yana nan.

Dariya salim yayi,haidar ya harare shi ya wuce ya ja matar shi ya fita,murmushi farouk yayi sannan suka yi sallama suka wuce.

Da dare ciwo ya tashi humaira daga barci,cikin tsananin azaba ta fara tashin momma da yake anan tare suka kwana.

Rudewa momma tayi ta fita da sauri ta taso daddy haka suka dauke ta sai hospital,daf da asuba ta haihu,sai a lokacin hankalin momma ya kwanta sannan ta Kira su inna Mari ta gaya musu.

Kiran salim tayi tace"ka gawa dan uwan ka matar shi ta haihu namiji,ai da murna ya daga sumayya cak yana juyi da ita.

Nan ya Kira farouk ya gaya mishi murna kam ba'a magana,kan kice me maganar humaira ta haihu ya zaga ko'Ina a fadin adamawa harda kano da kaduna,kowa yaji sai yayi murna.

A ranar farouk ya juya shi da salim,haidar sai Washe gari sai suje shida faisal da ammar.

Suna isa garin suka Tarar da gidan cike kowa na kokarin daukar yaron,ganin anki miko musu yasa ya takawa salim kafa.

Salim yace"momma a miko mana yaron mana,harara ta galla mishi tace"da yake kai ne Mara kunya ko shi bazai iya magana ba shiyasa ya wakiltaka sannan duk nan ni ka raina shiyasa ni kace na miko muku to bana da hannu.

Inna hadiza tace"a'a maman baby ya za kice haka mana duk wanda ya mika yaron ai bai yi laifi ba",momma tace"amma me yasa bece umman su ba ko ke sai ni",dariya suka yi gaba daya,sannan inna hadiza ta dauki yaron ta mika musu.

Da sauri duka suka mika hannu,farouk ya juya ya kalli momma ganin shi take kallo yasa yayi

saurin saukar da kan shi  ya janye hannun shi,salim yasa hannu ya amsa.

Masha allah kawai ya furta domin yaron kyakkyawa dashi kamar farouk yayi kaki ya tofar,hudu ba yayi mishi sannan ya mikawa farouk.

Amsa yayi jiki a sanyaye,idanu ya tsura mishi,gaskiya yaron kyakkyawa ne,murmushi yayi yana dagowa suka hada ido da momma yayi saurin mikawa salim yaron yace "mai dashi mu tafi" .

Har sun mike inna hadiza tace"meye haka tun yanzu,salim ya tabe fuska yace"inna Dan allah ba dole mu tafi ba tun dazu momma ke wa Dan uwa wani kallo wanda yasa duk ya tsargu ni gani nake kamar laifi muka yi Mata ma kice tayi hakuri mun tafi.

Sai kuma jikin su duka yayi sanyi momma a ranta tace"wato yana sane kenan,wannan wane kalan so ne suke wa juna.

Inna hadiza tace"a'a babu abinda kuka Mata Ku koma Ku zauna ko ganawa da matar ka baka yi ba sannan kace ka tafi gashi ma baka gaya mana sunan yaron ba".

Juyawa yayi ya kalli salim yace"ai ban San wane suna salim yasa musu ba",salim yace"sunan baffa ne fa wato adam",kowa yaji dadi shi kan shi farouk sunan daya ke so yasa wa yaron kenan.

Humaira kuwa fitowar ta daga wanka kenan,duka fita su kayi suka bar ta da mijin ta,rungume ta yayi yace"na gode teddy da wannan babyn da kika bani ban San me zan ce miki ba.

Murmushi tayi tace"nice da godiya kuma ni ya ka mata nayi farin ciki da samun ka a matsayin miji na.

Sai yamma sannan suka bar taraba,Washe gari su haidar suka zo suma suka ga baby.

Sai ana gobe suna sannan farouk ya sami damar komawa domin har tana kayan da zasu saka salim ya aika musu dashi akwati guda,da yaji labari murmushi kawai yayi.

Suma su sumayya ana gobe suna suka sami damar zuwa,yusra ta dauki yaron tace"masha allah ya sunan shi ne?",humaira tace"sunan baffa aka saka",sumayya tayi saurin amshewa tace"sai a rinka ce masa irfan",humaira tace"to.

*📑FAROUK KO  HAIDAR* 📑

*~GOLDEN PEN WRITERS ASSOCIATON~💫💫💫*

https://www.facebook.com/groups/1569379426621615/

*~❄we beare's of soon golden we writer's assiduously percieven No pain so magical Our creative golden pen Be hold our worlds A production of our pen savour Out worlds for it cause u np pain~*

written🖊 By Deeja One Love

Dedicated to madeena m umar🌹

75-76

*Last page*

Ranar suna gidan cike yake da jama'a,ana ta hada hada.

Mai jigo kuwa ta hade cikin wata dakakkiyar shadda ruwan golden tayi mata masifar kyau,haka uban gayya shima wankan shadda yayi sai da tashi sky blue ne(aradu ina so naga namiji yasa sky blue😁).

Humaira ta shiga wannan ta fita wancan domin kaya dai ta gansu Dan daddy hamma akwati biyu ya aiko mata da shi daya nata daya na baby haka ma mai martaba,daddyn yola da daddyn kaduna ma duka sun taka rawar gani.

Suna dai masha allah komai waja-waja domin duk wani abu na ci dana bukata an samar dashi wadatacce kowa yaci ya sha masha allah.

Satin ta biyu da haihuwa suka koma strike,wanda dole tasa ta komawa adamawa,amma momma sai da ta hada ta da wata yarinya mai kula da irfan.

Watan irfan takwas amma sai kace Wanda yafi shekara yayi bulbul dashi,karatu kuma yanzu babu kama hannu yaro domin tana samin kulawa sosai wajen farouk.

Shekarar irfan daya da wata bakwai humaira ta yaye shi,tana yaye shi farouk ya dauke shi ya kai shi taraba,itama humairan hakan yafi Mata domin tana bukatar hutawa.

Farouk ya shigo ya Tarar da ita sai barci take kwasa,murmushi yayi domin ganin project take yi amma barci ya dauke ta,dauke laptop din yayi ya karasa Mata.

Shida na yamma ya tashe ta,a gajiye ta tashi,sallah tayi kawai ta kwanta,shidai farouk be ce Mata komai ba.

Yau allah da ikon shi humaira da sumayya  an zama cikakkun  gynecology,alhamdulillahi sun fito da second class upper,duka har mutanen Zaria sun zo.

Dama aiki a hospital din su farouk za suyi.

Yau watan su daya da fara aiki,farouk ya bude kofa ya shiga office din humaira,tsabar aiki humaira bata dago ba,kujera ya ja ya zauna sai da ta gama sannan ta dago ta kalle shi tace"yadai meke damun ka,"ya mutsa fuska yayi yace"soyayyar ki mana.

Tashi tayi tazo ta zauna akan cinyar shi,hannun ta ta makalo ta wuyan shi ta fara aika mishi da kiss.

Bude kofar akayi aka shigo,da sauri suka waiga,haidar yace"amma Ku akwai yan duniya kun bar patients a waje kun zo kuna shan love ko?.

Dariya sukayi humaira tace"kai ma fa babu Wanda ya hanaka yin love din nan,".

Girgiza kai kawai yayi ya ajiye file din hannun shi yace"idan kin gama gashi sai Ki duba.

Wayar farouk tayi Kara ganin kiran momma ne yasa yayi saurin dagawa,gaishe ta yayi kafin tace"farouk Ku zo Ku dauki Dan Ku Dan ya ishe mu,farouk yayi murmushi yace"zan yiwa audu waya zai zo ya dauke shi Dan mu aiki ya mana yawa,daga haka ya kashe wayar.

BAYAN SHEKARA TARA

Wata mota ce Ferrari fara ta tsaya a bakin harabar gidan,yarane guda uku suka bude motar suka fito da gudu.
Bayan su wani Dan saurayi ne sai farouk daya riko mishi hannu.

Da sallama suka shiga gidan,a zaune suka sami humaira hannun ta rike da wata kyakkyawar yarinya,su kuma wa'inda suka shigo suna kasa kowa na kokawa da leda.

Farouk yace"mama na kawo na bude Mimi,cikin sauri karamar yarinyar ta mike ta nufi wajen shi.

Sallama salim yayi bayan shi sumayya ce sai yara guda biyar da suka biyo bayan su,da sauri humaira ta mike tana cewa"oyoyo takwara ta,"harararta sumayya tayi tace"to ban zo da ita ba.

Cikin sauri tace"saboda?",saboda kin fi son ta akai na,dariya suka yi duka kafin salim yace"ke kuma jealousy ko?.

Wasu yaran ne suka kuma shigo wa bayan su surayya ce,yau dai ziyara aka kawo mana kenan ko?dariya a kayi gaba daya.

Salim yayi sallama ya shigo,bayan sun zauna suka cigaba da hada-hada,wata yarinya ce ta shigo wacce ba zata wuce shekara goma sha hudu ba,ganin gidan a cike ta hade rai.

Farouk yayi murmushi yace"taho nan kinky,mikewa tayi a hankali taje. wajen shi,hannun shi ta rike tayi murmushi tace"FAROUK KO HAIDAR?"

Sakin baki suka yi sumayya cikin zafin rai tace"uban ki ne,dariya suka yi suka ce"ai baki yi karya ba,hannu ya mika mata suka tafa.

Murmushi haidar yayi yace"kuzo muyi selfie.
Duka matsawa sukayi.

Gefe na koma ina kallon ikon allah daga me tabe baki sai mai kwalalo idanu.

Dariya nayi nace"allah ya bar Ku tare masoya har abada.

Tammat bi hamdullahi.

Anan na kawo karshen littafi na mai suna
FAROUK KO HAIDAR.

Abin da nayi kuskure allah ka yafe mini.

Jinjina gare Ku kungiya daya tamkar da million GOLDEN PEN WRITERS ASSOCIATION kun

cancanci yabo daga gareni baku kyamar bako haka baku wulakanta karamin marubuci Allah ka Kara hade kanmu ameen

Jarumin admin din mu umar dalhat lallai ka cancanci yabo domin kana jajircewa wajen ganin typing din mu ya tafi yadda ya ka mata
Allah ya baka mata ta gari da 'ya'ya wainda zasu ji tausayin ka yasa ka gama da iyayen ka lafiya.ameen

Sister nabeela ubangiji allah ya baki lafiya yasa kaffara ne,group din sai yayi babu dadi da babu ke a ciki yini daya kawai gaskiya muna missing dinki,fatan mu allah ya tashi kafadun ki.

Sardaunan gauraye kai ma ina godiya a gare ka bashier sufyein(lazy writer)kawai.

Godiya gareku
Aeeshat Adam(daughter)
Marakisiyya mustapha.
Amatul manan
Shamsiyya m magaji
Khadeeja duhu
Aisha yunusa
Maryam khamis
Fatima hussein
Dijency

Members of

Sardauna myth
Aunty fati hausa novels
Dandalin littattafan jarumai and hausa novels
Hausa novels a yau
Hafsat hausa $h^2$ novels

Da sauran wainda ban samu damar ambatar su ba duka ku sani one love na sanku kamar yadda kuke sonta.

Ku kuma star boy umar da abubakar Ahmad na kusa aurar daku na huta ehe!

❤❤❤one love ❤❤for you guys and babs❤❤

Ramadan mufeeda in advance to all Muslim ummah all over d world.

Sai mun hadu bayan sallah idan muna da rai da lafiya.

*bye for now*